KOYARWA AKAN
BISHARA TA HANNUN

# YAHAYA



**Yesu ya ce mata, “Ai, ni ne tashin matattu, ni ne kuma rai. Wanda ya gaskata da ni, ko ya mutu zai rayu.”**

**—Yahaya 11:25**

# ME YA SA AKA RUBUTA BISHARA TA HANNUN YAHAYA?

**"Yesu ya yi waɗansu mu'ujizai da yawa dabam dabam a gaban almajiran, waɗanda ba a rubuta a littafin nan ba. Amma an rubuta waɗannan ne, domin ku ba da gaskiya Yesu shi ne Almasihu, Ɗan Allah, ta gaskatawa kuma ku sami rai a cikin sunansa."**

**–Yahaya 20:30, 31**

Yahaya da kansa ya ce, shi ne almajiri "wanda Yesu ke ƙauna." Ba mu yi tsammani Yesu ya fi ƙaunar Yahaya fiye da sauran almajiransa ba, amma kila Yahaya ya fi ƙaunarsa. Yahaya ya fi jin daɗin ƙaunar Yesu, shi kuma ya fi gane da dalilin zuwan Yesu da aikinsa a duniya.

Shekaru da dama bayan an rubuta Bishara ta Hannun Matiyu, da ta Markus, da ta Luka, wata koyarwa ta watsu cewa Yesu mutum ne. Yahaya ya rubuta wannan Bishara don ya bayyana Yesu, Allah ne, ya zo da jikin mutum. Daga cikin yawan abubuwa na banmamaki waɗanda Yesu ya yi, Yahaya ya rubuta su waɗanda suka tabbata lalle shi Ɗan Allah ne yadda ya faɗa.

Yahaya ya tabbatar da dalilan da shugabannin addini a wannan zamani suka ƙi Yesu, suka ba da shi domin a gicciye shi. Dalili ke nan, domin ya ce shi da Allah ɗaya ne! Yahaya ya nuna yadda Yesu yana da shiri ya zama Ɗan Rago na Allah mai ɗauke da zunubin duniya. Yesu ya ba da kansa hadaya mara aibi wanda Allah yake so domin ya fanshi mutanen duniya daga zunubansu.

Nufin Yahaya ne, kowa da ya karanta wannan Bishara (labari mai daɗi) ya gaskata Yesu, ya karɓi rai madawwami.

Addu'ata ke nan, wannan koyarwa ta Bishara ta Hannun Yahaya za ta bishe ku, ku gaskata Yesu Almasihu ku karɓe shi Mai Cetonku da Ubangijinku. Yesu Mai Rai ne, zai ba ku rai madawwami. Ko za ka faɗa masa cewa, "Yau na ƙi tsohon raina, na karɓi sabon rai cikin Yesu"? Ka yi masa godiya sabili da sabon rai da ya ba ka. Ka yi zumunci da shi kowace rana. Ka yi tafiya bisa ga nufinsa kowace rana. Ka shaida wa waɗansu cewa Yesu yana ƙaunace su kuma. **—(Mrs.) Vicky R. Benson**



# YADDA ZA KA YI NAZARIN MAGANAR ALLAH

**1. Ka roƙi taimakon Allah.** Kana bukatar taimakon Allah domin ka fahimta abin da kake nazarinsa. Ka yi addu'a da ke cikin Zabura 119:18. "Ka buɗe idona domin in ga gaskiyar shari'arka mai banmamaki."

**2. Ka karanta ayoyi a hankali a kaɗaice.** Ja layin ƙarƙashin kalmomi da ka fi lura da su. Ka tuna, Allah yakan yi magana da zuciyarmu ta wurin maganarsa.

**3. Ka ba da amsoshin tambayoyin da aka yi a littafin nan.** Za ka sami amsoshin daga cikin ayoyin da ka karanta.

**4. Ka daidaita amsoshinka da amsoshin da ke a bangon littafin nan na baya.**

**5. Ka haddace ayoyin da ke bayan kowane babi.** Karanta kowace aya sau da dama, har ka iya faɗe ta ba tare da dubawa ba. Kila za ka so ka rubuta ayar a kan wata ƙaramar takarda domin ka tafi da ita duk inda za ka tafi. Kowace rana ka faɗe ta. Ka faɗa wa wani ko wata domin ya duba takardarka ko ka yi kuskure. Ka maimaita ayar kowane mako, da kowane wata domin kada ka mantar da ita. Idan ka ajiye ayoyin a zuciyarka za ka gane maganarka da ayyukanka za su sāke. Ka zaɓi waɗansu ayoyi da za ka haddace kuma.

**6. Ka yi tunanin Maganar Allah da ka karanta, ka kuma haddace.** Allah ya yi alkawarai gare su waɗanda suke yin tunani a kan Maganarsa:


> Kada wannan littafin dokoki ya rabu da bakinka, amma zai zama abin da za ka yi ta tunani a kansa dare da rana domin ka kiyaye, ka kuma aikata bisa ga dukan abin da aka rubuta a ciki, gama ta haka za ka yi albarka cikin hanyarka, ta haka kuma za ka yi nasara.
>
> –Joshuwa 1:8

> Maimakon haka, yana jin daɗin karanta shari'ar Allah, yana ta nazarinta dare da rana. Yana kama da itacen da ke a gefen ƙorama, yakan ba da 'ya'ya a kan kari, ganyayensa ba sa yin yaushi, yakan yi nasara a dukan abin da yake yi. –Zabura 1:2, 3

**7. Yi aniya ka aikata abin da Allah ya faɗa.** Yakubu 1:22 ya ce, "Amma ku zama masu aikata maganar, ba masu ji kawai, kuna yaudarar kanku ba." Yesu ya kwatanta mutum wanda ya ji magana amma bai aikata ba da wawan mutum da ya gina gidansa a kan rairayi. Da ruwa ya sauƙo gidan ya rushe. Amma mutum, ko mace, ko yaro wanda ya ji maganar Yesu, ya aikata kuma, an kwatanta shi da mutum mai hikima, wanda ya gina gidansa bisa fa. Sa'ad da ruwa ya sauƙo ya bugi gidansa bai faɗi ba. Sai mu yi biyayya ga abin da Allah ya faɗa sa'an nan za mu ci gaba cikin Almasihu, mu ƙaru da sanin Allah. Ka rubuta abin da za ka yi, sa'an nan ka yi shi. Allah zai taimake ka.

**8. Ka shaida Maganar Allah ga waɗansu.** Kila za ka so ka faɗa wa waɗansu cikin iyalinka abin da ka koya daga cikin Maganar Allah. Maimaitawar Shari'a 6:7 ta ce, "Sai ku koya wa 'ya'yanku su da himma. Za ku haddace su sa'ad da kuke zaune a gida, da sa'ad da kuke tafiya, da sa'ad da kuke kwance, da sa'ad da kuka tashi."

# LABARI NA 1. AN GABATAR DA YESU ALMASIHU



Yahaya 1:1-18
[1]Tun fil azal akwai Kalma,
Kalman nan kuwa tare da Al-
lah yake, Kalman nan kuwa
Allah ne. [2]Shi ne tun fil azal
yake tare da Allah. [3]Dukan a-
bubuwa sun kasance ta gare shi
ne, ba kuma abin da ya kasance
na abubuwan da suka kasance,
sai ta game da shi. [4]Shi ne
tushen rai, wannan rai kuwa shi
ne hasken mutane. [5]Haske na
haskakawa cikin duhu, duhun
kuwa bai rinjaye shi ba.
[6]Akwai wani mutum da Allah
ya aiko, mai suna Yahaya. [7]Shi
fa ya zo shaida ne, domin ya
shaidi hasken, kowa yǎ ba da
gaskiya ta hanyarsa. [8]Ba shi ne
hasken ba, ya zo ne domin ya
shaidi hasken. [9]Akwai hakika-
nin haske mai shigowa duniya
da ke haskaka kowane mutun.
[10]Dā yana duniya, duniyar ma
ta wurinsa ta kasance, duk da
haka duniya ba ta san shi ba.
[11]Ya zo ga abin mulkinsa ne,
jama'a tasa kuwa ba ta karɓe
shi ba. [12]Amma duk iyakar
waɗanda suka karɓe shi, wato
masu gaskatawa da sunansa, ya
ba su ikon zama 'ya'yan Allah,
[13]wato waɗanda aka haifa ba
daga jini ba, ba daga kwaɗayin
jiki ko nufin mutum ba, amma
daga wurin Allah. [14]Kalman nan
kuwa ya zama mutum, ya zauna
a cikinmu, yana mai matuƙar
alheri da gaskiya. Mun kuma
dubi ɗaukakarsa, ɗaukaka ce
ta makaɗaicin Ɗa daga wurin
Ubansa.
[15]Yahaya ya shaide shi, ya
ɗaga murya ya ce, "Wannan shi
ne wanda na ce, 'Mai zuwa ba-
yana ya zama shugabana, domin
dā ma yana nan tun ba ni.'"
[16]Dukanmu kuwa daga falala
tasa muka samu, alheri kan al-
heri. [17]Domin Shari'a ta han-
nun Musa aka ba da ita, alheri
da gaskiya kuwa ta wurin Yesu
Almasihu suka kasance. [18]Ba
mutumin da ya taɓa ganin Al-
lah daɗai. Makaɗaicin Ɗa, wan-
da yake yadda Allah yake, wan-
da kuma yake a wurin Uba, shi
ne ya bayyana shi.

## Abin da za ka Yi

A. Ka rubuta amsar kowace tambaya. In ba ka san amsa ba, ka sāke karanta labarin.

I. Wanene shi ne "Kalma"?____________(aya ta 1)

2. Ina "Kalma" yake?__________ __________(1)

3. Wanene "Kalma"?____________(4)

4. Ina ne Kalma ke haskaka? Cikin____________(5)

5. Wa Allah ya aiko domin ya shaida hasken? Wani mutum sunansa____________(6).

[Wannan Yahaya Mai Baftisma ne, ba Yahaya wanda ya rubuta wannan Bishara ba.]

6. Suwanene ba su karɓi Yesu ba?____________(11).

[Isra'ilawa–waɗanda Allah ya zaɓa–ba su karɓe shi ba.]

7. Ina ikon da aka ba su waɗanda suka karɓi Yesu? Ya ba su ikon__________ _____ __________(12).

8. Su waɗanda aka haifa daga wurin Allah, "waɗanda aka haifa ba____________ba, ba daga____________ko__________ ba, amma daga wurin__________"(13).

[Sa'ad da waɗansu suka zama 'ya'yan Allah, abin banmamaki ne wanda Allah kansa ya yi. Ba domin an haife su wurin iyaye masu bi ba, ko domin su da kansu ke so, ko domin suna so su zama masu bin Yesu. Sabuwar haihuwa ta wurin Allah, ita ce aikin Allah kaɗai.]

9. Me "Kalman nan" ya zama?____________(14)

10. Ina ne "Kalman" yake da zama?________________(14)

11. Ina abu biyu da muka karɓa sa'ad da muka karɓi Almasihu? "Dukanmu kuwa daga______________muka samu,__________ __________kan____________"(16).

12. Da ya ke babu wanda ya taɓa ganin Allah, wa ya zo domin ya bayyana shi? Makaɗaicin____________(18).

[Domin Yesu shi ne Allah, yana da iko a nan duniya lokaci dai-dai da yake tare da Uban, inda yake tun fil azal. (Gwada aya ta 18 da aya ta 1.)]

B. Ka rubuta ayan nan, ka haddace ta: **Yahaya 1:12.**

## Yesu Allah Ne—Ya Zo da Jikin Mutum

Kafin mu iya karɓar Yesu, mu gaskata shi, sai mu san kowa-nene shi. Aya ta 18 ta ce Yesu ya zo ya bayyana mana Allah, domin ba wanda ya taɓa ganin Allah. Ɗaukakarsa yana haskaka ba misali. Tsarkinsa ya wuce ganewa.

Saboda mutum mai zunubi ne, yakan zama a duhu. Duhu a duniyan nan yakan sa mutum ya ƙyale Allah, ya yi zaman kansa aya ta 5 ta ce, duhun kuwa bai rinjaye shi ba.

Littafi Mai Tsarki ya ce, **"Allah haske ne, ba kuwa duhu gare shi ko kaɗan"** (1 Yahaya 1:5b). An ce da Yesu **"hakikanin haske"** yadda aka ce da Allah. Ta wurin wannan **hakikanin haske** mutum yakan ga kansa mai zunubi ne. Ta wurin wannan **hakikanin haske** kuma, yakan gane yadda Allah yake. Ya iya gane kuma yadda ya kamata ya zama.

Abin murna ne wannan hakikanin haske (Yesu) yakan haskaka cikin duhu na wannan duniya, ya bayyana mana Allah. Wata ya-rinya ta ce, "Yesu hoto ne mafifici wanda Allah ya yi!" Yesu ho-ton Allah ne —wani wanda mutum ya iya gani, ya iya ji, ya iya taɓa.

Yesu ya zauna wurin mutane. A Tsohon Alkawari alfarwa ta sujada ita ce wurin da Allah ya zauna da mutanensa. Sa'ad da suka tashi tafiya zuwa wani wuri, suka dauƙi alfarwa ta sujada tare da su. Lokacin da Isra'ilawa suka yi zunubi ɗaukakar Allah ta tashi daga alfarwa ta sujada, ko daga baya daga haikali na Allah da ke tsakiyarsu. Abin tausayi ne mutane da yawa ba su gane da shi ba. Dukansu da suka gaskata Allah suka ga ɗau-kakarsa cikin Yesu lokacin da yake duniya.

## Yesu shi ne Kalmar Allah

Littafi Mai Tsarki ya ce, **"Maganarka fitila ce wadda za ta bi da ni, haske ne kuma a kan hanyata"** (Zabura 119:105). Wata suna na Yesu shi ne "Kalmar Allah." (Gwada aya ta 1 da ta 14.) Littafi Mai Tsarki shi ne Maganar Allah a rubuce. Yesu shi ne Maganar Allah rayayye, domin Allah ya bayyana kansa ta wurin Yesu.

**"A zamanin dā, Allah ya yi wa kakannin kakanninmu magana ta hanyoyi masu yawa iri iri, ta bakin annabawa, amma a zamanin nan na ƙarshe sai ya yi mana magana ta wurin Ɗansa"** (Ibraniyawa 1:1, 2a).

## Yesu shi ne Rai na Allah

Ka taɓa yi tunani cewa, me ya sa muka zama 'ya'yan Allah sa'ad da muka karɓi Yesu a zuciyarmu? Dalili ke nan, **"shi ne tushen rai"** (aya ta 4).

Da fari, muka gane ta wurin Yesu dukan abubuwa sun kasance. (aya ta 3 da ta 10). **"Wato dukkan abubuwa an halicce su ne ta wurinsa, shi ne kuma makoma tasu. Shi ne gaba da dukkan abubuwa, dukkan abubuwa kuma shi ne ke riƙe da su"** (Kolosiyawa 1:16b, 17). Yesu, kamar Allah, shi ne tushen rai. Shi kuma yana riƙe rai. **"Shi kansa ne ke ba dukkan mutane rai, da numfashi, da dukkan abubuwa. Domin 'Ta gare shi ne muke rayuwa, muke motsi, muka kuma kasance'"** (Ayyukan Manzanni 17:25b, 28a).

Yadda mutum ya zama rayayyen mai rai sa'ad da Allah ya hura masa numfashin rai lokacin da ya halicce shi, haka kuma an ba Yesu iko ya ba su da suka karɓe shi sabon rai madawwami (Yahaya 17:2). **"Duk wanda ke da Ɗan, yana da rai. Wanda ba shi da Ɗan Allah kuwa, ba shi da rai"** (1 Yahaya 5:12).

Kai, ka taɓa karɓar sabon rai? Ka gaskata Yesu ya ba ka rai madawwami? Idan ka yi, ka zama cikin 'ya'yan Allah. Kana da nasa rai a cikinka. Idan ka yi zamanka cikin haskensa za ka karɓi albarka bisa albarka (aya ta 16). Idan kai ba ka karɓe shi ba, sai ka roƙe shi yanzu ya ba ka wannan rai–ran nan madawwamiya.

Ko ka taɓa amsa gaisuwa a ƙofarka? Yesu yana tsaye wurinka yanzu, yana ƙwanƙwasa a ƙofar zuciyarka. Alkawarinsa ne, **"Kowa ya ji muryata ya buɗe ƙofar, sai in shiga wurinsa"** (Wahayin Yahaya 3:20b).

## LABARI NA 2. YAHAYA MAIBAFTISMA YA SHIRYA TAFARKIN ZUWAN YESU




Yahaya 1:19-34

19Wannan kuwa ita ce shai-
dar Yahaya, wato sa'ad da Ya-
hudawa suka aiki firistoci da
Lawiyawa daga Urushalima su
tambaye shi, ko shi wanene.
20Sai ya faɗi gaskiya, bai yi
musu ba, gaskiya ya faɗa ya
ce, "Ba ni ne Almasihu ba."
21Sai suka tambaye shi, "To,
yaya, Iliya ne kai?" Ya ce,
"A'a, ba shi ba ne." Suka ce,
"Kai ne annabin nan?" Ya ce,
"A'a." 22Sai suka ce masa, "To,
wanene kai, domin mu sami
amsar da za mu mayar wa
waɗanda suka aiko mu? Me
kake ce da kanka?" 23Ya ce,
"Ni murya ce ta mai kira a
jeji, mai cewa, 'Ku miƙe wa
Ubangiji tafarki,' yadda An-
nabi Ishaya ya faɗa." 24Su ku-
wa, Farisiyawa ne suka aiko
su. 25Sai suka tambaye shi suka
ce, "To, don me kake yin baf-
tisma in kai ba Almasihu ba
ne, ba kuwa Iliya ba, ba kuma
annabin nan ba?" 26Sai Yahaya
ya amsa musu ya ce, "Ni kam,
da ruwa nake baftisma, amma
da wani nan tsaye a cikinku
wanda ba ku sani ba, 27shi ne
mai zuwa bayana, wanda ko
maɓallin takalminsa ma, ban
isa in ɓalle ba." 28An yi wan-
nan a Betanya ne, a hayin Ko-
gin Urdun, inda Yahaya ke yin
baftisma.

29Kashegari Yahaya ya tsin-
kayo Yesu na nufo shi, sai ya
ce, "Kun ga, ga Ɗan Rago na
Allah, mai ɗauke zunubin du-
niya! 30Wannan shi ne wanda

na ce, 'Wani mutum na zuwa bayana, wanda ya zama shugabana, domin dā ma yana nan tun ba ni.' 31Dā kam, ban san shi ba, sai domin a bayyana shi ga Isra'ila ne na zo, nake baftisma da ruwa." 32Yahaya ya yi shaida ya ce, "Na ga Ruhu na saukowa kamar kurciya daga sama, ya kuma zauna a kansa. 33Dā kam, ban san shi ba, sai dai wanda ya aiko ni in yi baftisma da ruwa, shi ne ya ce mini, 'Wanda ka ga Ruhun na sauko masa, yana kuma zama



a kansa, shi ne mai yin baftisma da Ruhu Mai Tsarki.' 34Na kuwa gani, na kuma yi shaida, cewa wannan Ɗan Allah ne."

## Abin da za ka Yi

Ka cika filaye da kalma wanda ke daidai.

1. Yahaya Maibaftisma ya ce shi____________ce ta mai kira a______________(23).
2. Yahaya Maibaftisma ya maimaita maganar Annabi Ishaya da ya ce, "ku____________wa____________tafarki" (23).
3. Yahaya Maibaftisma ya ce, ko Yesu ya zo____________ ya zama____________(27, 30).

[Wato Yahaya Mai baftisma ya zo domin ya shirya tafarkin Yesu, Yesu ya fi shi girma. Yahaya ya ce shi bai isa ya yi aikin bawa ya ɓalle maɓallin takalminsa ba. Yahaya ya san girman Yesu.]

4. Sa'ad da ya bayyana Yesu ga dukan mutane, ya ce da shi ____________na____________, mai ɗauke____________ ____________(29).
5. Yahaya Maibaftisma ya yi baftisma da ruwa domin ya bayyana shi ga______________(31).

6. Yahaya Maibaftisma ya tabbata Yesu Ɗan Allah ne (haifaffe kamar mutum) domin Ruhun Allah ya sauko daga sama kamar ________________ ya kuma zama a kansa (32). Wannan alama ce cewa Yesu zai yi baftisma da ________________________ (33).

## Shirin Tafarkin Yesu

Shekara ɗari huɗu ne, Isra'ilawa, zaɓaɓɓun Allah, ba su da wani annabi da zai ba su maganar Allah ba. Suna da Tsohon Alkawari da ya nuna masu alkawalolin Allah da abin da yake so su yi. Sun sani Almasihu, wanda zai cece su, zai zo ya mallake su wata rana. Ishaya ya ce budurwa za ta haife shi, za a ce da shi Immanuel, wato Allah tare da mu (Ishaya 7:14). Annabi Mika kuma ya ce za a haife shi a Baitalami zai sarauci Isra'ila (Mika 5:2).

Ko kake cewa mutane suka yi mamaki, suka yi murna kuma da Yahaya Maibaftisma yana yin wa'azi cewa, su shirya tafarkin Ubangiji? Yaya mutane za su yi shiri? Matiyu ya gaya mana cewa, Yahaya Maibaftisma ya zo, yana yin wa'azi cewa, **"Ku tuba, domin Mulkin Sama ya kusato"** (Matiyu 3:2b). Mutane da yawa suka faɗi zunubansu, sa'an nan Yahaya Maibaftisma ya yi masu baftisma cikin Kogin Urdun. Kafin zukatanmu a shiryayye suke, sai mu tuba, mu faɗi zunubanmu, mu rabu da su, sa'an nan mu karɓi Yesu Mai Cetonmu. Sa'ad da muka yarda mu rabu da zunubanmu, da tunaninmu marasa kyau waɗanda muke da su gaban Allah da mutane, sa'an nan a shiri muke, mu karɓi Yesu, hanya zuwa wurin Allah, Sarkinmu da Ubangijinmu. Baftismar Yahaya da ruwa ya kwatanta mana wanken zunubanmu. Yesu ya yi baftisma da Ruhu Mai Tsarki, ya tsarkake mu sai ka ce da wuta (Matiyu 3:11, 12) zai ba mu sabon rai na adalci. (Rai na Yesu a cikinmu.)

Ka taɓa faɗa wa Allah zunubanka?

## Yesu, Ɗan Rago na Allah

Isra'ilawa sun san muhimmancin ɗan rago cikin sujadarsu na Tsohon Alkawari. Sa'ad da suke yin bauta, Allah ya zuga zuciyar Fir'auna a Masar ya yarda su Isra'ilawa su fita ƙasarsa. Allah ya aiko masa annoba goma kafin Fir'auna ya yarda wajen mutum zambar dubu biyu su fita. Annoba na ƙarshe, shi ne na mutuwa cewa, ɗan fari na kowane gida, mutum da dabba, za su mutu sa'ad da Ubangiji na ratsa wurin.

Amma akwai hanyar tsira. Kowace gida da ta yi biyayya ga maganar Allah za ta tsira. Allah ya ce su ɗauki ɗan rago marar aibi, su yanka, su sa jininsa a dogaran ƙofa da kuma kan ƙofar gidajensu. Sa'ad da Ubangiji ya ga jinin ɗan ragon zai ketare wurin, ɗan fari ba zai mutu ba. Wannan shirin Allah



ke nan. Daga baya Isra'ilawa suka kiyaye ranar nan domin su tuna yadda Allah ya ketare gidajen Isra'ilawa a Masar bai taɓa gidajensu ba. (Za a iya karanta labarin nan a Fitowa 12:1-42.)

Daidai ne Yahaya Maibaftisma ya ce da shi "Ɗan Rago na Allah". Yesu ya zo domin ya zama hadaya mara aibi, ya ba da jininsa domin mu–domin lokacin da shari'ar Allah ya faɗo ga masu zunubi zai tsallake masu adalci. Ibraniyawa 9:22 ya ce, **"In ba game da zubar da jini ba kuwa, ba gafara."** Littafin Firistoci 17:11 ya ce, **"...gama da jini ake kafara saboda akwai rai a cikinsa."** Dukan raguna da su Isra'ilawa suka yanka shekara da shekara suka kwatanta Yesu, wanda zai zo ya zama "Ɗan

Rago na Allah". Ya ba da jininsa domin dukan wanda ya karɓe shi Mai Cetonsa, za a wanke su da jinin Yesu. **"Lalle hakika, ina gaya muku, duk mai jin maganata, yake kuma gaskata wanda ya aiko ni, yana da rai madawwami. Ba za a yi masa hukunci ba, domin ya riga ya tsere wa mutuwa, ya kai ga rai"** (Yahaya 5:24).

Ishaya 53:7 ya ambace shi cewa, **Kamar ɗan rago wanda ake shirin yankawa."** Yesu ya zo domin ya mutu saboda zunubin duniya. Sai a yi masa godiya yanzu domin ya zo, ya ba da jininsa dominka, ya wanki zunubanka. Sa'ad da Allah ya ga jininsa a zuciyarka, ba zai ga zunubanka kuma ba. Ya ga jinin Yesu, wanda ya ɗauki zunubanka a kansa, ya karɓi shari'arka a kansa. Godiya ga Allah!



**Ko kun zo gun Yesu domin gafara?**
**Yana kiranmu duka mu zo,**
**Shi ya ba da ransa domin dukanmu,**
**Sai ku zo wurin Yesu, ku zo.**

**SULHUNTA shi ne zaman ɗaya da Allah domin jinin Yesu ya tsarkake mu daga dukan zunubanmu.**

## LABARI NA 3. KARUWAR SANIN YESU



**Yahaya 1:35-49**

**35Kashegari kuma Yahaya na tsaye da almajiransa biyu. 36Yana duban Yesu na tafiya, sai ya ce, "Kun ga, ga Ɗan Rago na Allah!" 37Almajiran nan biyu suka ji ya faɗi haka, sai suka bi Yesu. 38Yesu ya waiwaya ya ga suna biye da shi, sai ya ce musu, "Me kuke nema?" Suka ce masa, "Ya Rabbi, wato Malam ke nan, ina kake da zama?" 39Sai ya ce musu, "Ku zo ku**

gani." Sai suka je suka ga inda yake da zama, suka kuwa yini tare da shi. Wajen ƙarfe huɗu na yamma ne kuwa. [40]Daya daga cikin biyun nan da suka ji maganar Yahaya suka kuma bi Yesu, Andarawas ne, ɗan'uwan Bitrus. [41]Sai ya fara samo ɗan'uwansa Bitrus, ya ce masa, "Mun sami Almasihu," wato shafaffe. [42]Sai ya kai shi wurin Yesu. Yesu ya dube shi, ya ce, "Wato kai ne Saminu ɗan Yahaya? Za a kira ka Kefas," wato Bitrus.

[43]Kashegari Yesu ya yi niyyar zuwa ƙasar Galili. Sai ya sami Filibus, ya ce masa, "Bi ni." [44]Filibus kuwa mutumin Betsaida ne, garin su Andarawas da Bitrus. [45]Filibus ya sami Nata'ala, ya ce masa, "Mun sami wanda Musa ya rubuta labarinsa a Attaura, annabawa kuma suka rubuta labarinsa, wato Yesu Banazare, ɗan Yusufu." [46]Nata'ala ya ce masa, "A iya samun wani abin kirki a Nazarat kuwa?" Sai Filibus ya ce masa, "Taho dai, ka gani." [47]Yesu ya ga Nata'ala na nufo shi, sai ya yi zancensa ya ce, "Kun ga, ga Ba'isra'ile na gaske wanda ba shi da ha'inci!" [48]Nata'ala ya ce masa, "A ina ka san ni?" Yesu ya amsa masa ya ce, "Tun kafin Filibus ya kira ka, sa'ad da kake gindin ɓaure ma, na gan ka". [49]Sai Nata'ala ya amsa masa ya ce, "Ya Shugaba, kai Ɗan Allah ne! Kai Sarkin Isra'ila ne!"



## Zo ka Gani

Almajirai guda biyu na Yahaya Maibaftisma suna so su ƙaru da sanin Yesu sa'ad da suka ji Yahaya cewa, "Kun ga, ga Ɗan Rago na Allah!" Suka yi shawara, suka bi shi, su san inda yake zama. Yesu ya ce musu, "Ku zo, ku gani." Ka iya yin tunani akan zancen da suka yi da Yesu! Lalle sun ƙaru dayawa a wurinsa, domin bai daɗe ba, ɗaya daga cikinsu, wato Andarawas, ya gaya wa ɗan'uwansa Bitrus cewa, "Mun sami Almasihu."

Ma'anar Almasihu "shafaffe ne."–wato mutumin da Allah zai aiko ya zama annabi, wato firist, ko sarki wanda zai mallaki mutanen Isra'ila. Annabawa da dama na Tsohon Alkawari suka yi magana batun wannan mutumin wanda zai zo. Ko Musa ma, ya rubuta zancensa Allah ya yi magana da Musa cewa, **"Zan tayar musu da wani annabi kamarka daga cikin 'yan'uwansu. Zan sa magana a bakinsa, zai faɗa musu duk abin da na umarce shi"** (Maimaitawar Shari'a 18:18). Daga baya Yesu ya ce, **"Yadda Uba ya koya mini, haka nake faɗa"** (Yahaya 8:28b). Lalle hankalin mutanen nan ya tashi!

Kai, fa? Ko kana so ka ƙaru da sanin Yesu? Kakan yi tunani cewa, "Wanene shi?" Yesu yana ce maka, "Yau, ka zo ka gan ni." Akan samu ta wurin nema. Yesu ya ce, **"Ku yi ta nema za ku samu"** (Matiyu 7:7b). Idan ka zo gun Yesu, za ka gani! In ka zama tare da shi, ka yarda ya yi maka zance ta wurin maganarsa zai nuna maka, shi wanene ne. Ka iya saninsa, kai da kanka! **"Zan ba su zuciyar da za su sani ni ne Ubangiji. Za su kuwa zama jama'ata, ni kuwa zan zama Allahnsu, gama za su komo wurina da zuciya ɗaya"** (Irmiya 24:7).

## Zancen da aka Shaida akan Yesu

Sa'ad da wani ya zo wurin Yesu, ya gane shi kowanene ne, yana so ya gaya wa waɗansu batunsa. Yana so ya gaya wa waɗansu abin da ya sani batun Yesu, domin abokansa su 'zo su gani' kuma. In ka san Yesu, kana ƙara koyo daga wurinsa, kakan shaida wa waɗansu wannan labari mai daɗi?

## Ka rubuta nan cewa Yesu wanene a saninka:

________________________________________

________________________________________

________________________________________

Ka roƙi Allah ya ba ka dama ka shaida wa wani yau, domin shi ya zo ya gani kuma.

# LABARI NA 4. YESU YA KAWO MURNA LOKACIN AURE



Yahaya 2:1-11

[1]A rana ta uku sai aka yi bikin aure a Kana ta ƙasar Galili. Uwar Yesu kuwa tana nan, [2]aka kuma gayyaci Yesu da almajiransa. [3]Da ruwan inabi ya gaza, uwar Yesu ta ce masa, "Ba su da sauran ruwan inabi." [4]Yesu ya ce mata, "Iya, ai, wannan magana ba taki ba ce. Lokacina bai yi ba tukuna." [5]Sai uwa tasa ta ce wa barorin, "Duk abin da ya ce ku yi, sai ku yi." [6]A wurin kuwa akwai randuna shida na dutse a ajijjiye, bisa ga al'adar Yahudawa ta tsarkakewa, kowacce na cin wajen tulu shida shida. [7]Sai Yesu ya ce musu, "Ku cika randunan nan da ruwa." Suka ciccika su fal. [8]Sa'an nan ya ce musu, "To, yanzu ku ɗiba, ku kai wa uban bikin." Sai suka kai. [9]Da uban bikin ya kurɓi ruwan da yanzu aka mayar ruwan inabi, bai kuwa san inda aka samo shi ba (amma barorin da suka ɗebo ruwan sun sani), ya yi magana da ango, [10]ya ce, "Kowa, ai, kyakkyawan ruwan inabi yakan fara bayarwa, bayan mutane sun shassha, sa'an nan kuma ya kawo wanda ya gaza na farin kyau. Amma kai ka ɓoye kyakkyawan ruwan inabin sai yanzu!" [11]Wannan ce mu'ujizar farko da Yesu ya yi, ya kuwa yi ta ne a Kana ta ƙasar Galili, ya bayyana ɗaukakarsa. Almajiransa kuma suka gaskata da shi.

## Abin da za ka Yi

Ka cika filayen nan da kalmomi daga cikin labarin.

1. Uwar Yesu ta ce wa barorin, "____________________________________________." (aya ta 5)
2. Sa'an da Yesu ya gaya wa barorin su cika randuna, suka ciccika su________________________." (aya ta 7)

## Biyayya shi ne Mabuɗin yin Murna

Ya yiwu Uwar Yesu ba ta taɓa ga Yesu ya aikita al'ajibi kafin wannan lokaci ba. Amma ta sani Yesu zai yi taimako. Mun sani ruwan inabi da suka sha a wannan lokaci ba irin da zai sa mutane su maye ba. Kuma ba irin da mutane suke yi yau ba. Shi ne ruwan inabi kurum, yana da daɗi. Lalle za a sha kumya in ya gaza.



Kila kai mai bi ne. Wani abu ya taɓa gaza maka? Hanƙuri yakan ƙare maka? Zuciyarka ta rasa murna ko ƙamna yanzu? Yesu yake ganin bukatarka, ko menene shi ke. Yana so ya albarkace ka da wani abin mamaki. Shi bai so ka taɓa sha kumya domin ba ka da isashen murna, ko salama, ko ƙamna don yini ba. Shi ya yi alkawali cewa, **"Duk mai gaskatawa da shi, ba zai kunyata ba"** (Romawa 9:33b). Amma akwai wani asiri kana bukata ka sani! Biyayya shi ne mabuɗin albarka! **"Duk abin da ya ce ku yi, sai ku yi."** Sa'an da muka yi biyayya, Yesu ya iya aika abin mamaki. Biyayya yakan nuna lalle muna gaskata shi.

Idan wani ya yi maka laifi, ka kan yi masa gafara (Matiyu 6:14-15)? Kana tara wa kanka dukiya a sama (Matiyu 6:20)? Kila ka yi tsammani ba ka iya ka bayar ga aikin Allah ba. Amma Yesu ya san bukatarka. Ka dogara gareshi ta wurin biyayya. **"Ku gwada ni, za ku gani, zan buɗe taskokin sama in zubo muku da albarka mai yawan gaske"** (Malakai 3:10b).

Allah yake ce maka yau, **"Sai dai ku cika da Ruhu"** (Afisawa 5:18). Babu wani mai bi da zai iya rayewa da murna yau, idan bai yarda Allah ya cika shi da Ruhunsa kowace rana ba.

Kila kai ba mai bi ba ne. Kila ba kake jin daɗin rai sosai ba. Kai kuma, ka iya yi biyayya ga umurnin Yesu. Zo gareshi, ka karɓi rai a yalwace. Ya ce, **"Ni kuwa na zo ne domin su sami rai, su kuma same shi a yalwace"** (Yahaya 10:10b).

Barori suka yi biyayya sosai. Su ba su cika tulun rabi rabi ba, ko kuwa kusa kusa ba. Suka cika su fal. In ka yi biyayya ga Allah da zuciya ɗaya, zai kawo murna da albarka. **"Kome za ku yi, ku yi shi da himma kuna bauta wa Ubangiji ne, ba mutum ba, da ya ke kun sani Ubangiji zai ba ku gādo sakamakonku. Ubangiji Almasihu kuke bauta wa fa!"** (Kolosiyawa 3:23, 24).

Akwai abin da Yesu ya nuna maka ya kamata ka yi? In haka ne, me ya sa ba za ka yi shi yau ba?

Sa'an da almajirai suka ga abin mamaki da Yesu ya yi ban gaskiyarsu ta fi na dā ƙarfi—suka gaskata shi. Sa'an da ka yi biyayya ga maganar Allah, ka ga abin da Allah ya yi, ban gaskiyarka za ta ƙara yawa kuma. Ban gaskiya kamar tsoka a jikinka ne. Ta kan ƙara ƙarfi ta wurin yin amfani da ita. Sai ka hore ta. Bari mu yarda, mu yi tafiya ta wurin bangaskiya kowace rana. **"Wanda yake da adalci ta wurin bangaskiya zai rayu"** (Romawa 1:17).

**BANGASKIYA** = Rabu Da Kome. Dogara Gareshi.

## LABARI NA 5. YESU YA TSARKAKE HAIKALI



**Yahaya 2:13-22**

**[13]Idin Ketarewa na Yahudawa ya matso, sai Yesu ya tafi Urushalima. [14]A cikin Haikali ya sami waɗansu dillalan shanu, da na tumaki, da na tattabarai, da kuma 'yan canjin kuɗi zaune wurin aikinsu. [15]Sai ya tuka bulala mai harsuna ta igiya, ya kore su duka daga Haikalin, har da tumakin da shanun, ya kuma watsar da kuɗin 'yan canjin, ya birkice teburorinsu. [16]Ya ce da dillalan tattabarai, "Ku kwashe waɗannan daga nan, kada ku mai da Haikalin Ubana kasuwa." [17]Sai almajiransa suka tuna a rubuce yake cewa, "Kishin Haikalinka ya ci raina matuƙa." [18]Sai**

Yahudawa suka amsa masa
suka ce, “Wace mu’ujiza za ka
nuna mana da kake haka?”
19Yesu ya amsa musu ya ce,
“Ku rushe haikalin nan, ni
kuwa in ta da shi a cikin kwa-
na uku.” 20Yahudawa suka ce,
“Sai fa da aka shekara arba’in
da shida ana ginin Haikalin
nan, kai kuwa a cikin kwana
uku za ka ta da shi?” 21Amma
haikalin da Yesu ya ambata ji-
kinsa ne. 22Saboda haka bayan
an tashe shi daga matattu, al-
majiransa suka tuna ya faɗi
haka, suka kuma gaskata Nassi
da maganar da Yesu ya faɗa.

## Abin da Yesu ya Sani

Ka tuna ma’anar Idin Ketarewa? Mun ambace shi akan shafe ta 10. Yesu ya tafi Urushalima don ya kiyaye Idin Ketarewa. Abin da ya sami cikin Haikali, abin mamaki ne! Bai zama kamar wurin su’jada ba, ko wurin da za a yi shiri da Allah ba. Ya zama kamar babban kasuwa! Yesu ya ji haushi ƙwarai.

Gaskiya ce, mutane suke da bukata su sayi namomi domin su yi hadaya ga Allah da su. Amma masu sayarwa suke yi musu rikici domin suke sa masu kuɗi dayawa wanda bai kamata ba. Suke sayar da su cikin Haikali! Ba abin mamaki ba ne, Yesu ya ƙore su daga cikin Haikali! An rubuta cikin Markus 11:17b, **“Ashe, ba a rubuce yake ba cewa, ‘Za a kira masujadata ɗakin addu’a na dukkan al’ummai’? Amma ku kun maishe shi kogon ’yan fashi.”**

Yesu ya gaya wa shugabannin Yahudawa daidai ne ya tsarkake Haikali domin za a tabbatad da wannan lokacin da sun rusad da haikalin. Shi Yesu, zai tashe shi kuma cikin kwana uku! Suka yi mamaki domin ba su sani Yesu yana ambaton jikinsa ba. Yesu ya sani shugabannin Yahudawa ɗin za su gicciye shi. Ya sani kuma bayan kwana uku zai ta da jikin kansa daga matattu.

## Jikin Yesu Haikalin Allah Ne

Shekaru dayawa kafin wannan lokaci, haikali ɗin nan mai kyau ne. Sulemanu ya gina shi. Allah ya cika shi da darajarsa. Amma domin mutanen jama’ar Isra’ila suka bi alloli, darajar Allah ta rabu da haikalin, an rushe shi kuma. Daga baya su waɗanda suke

so su bi Allah, suka sake gina shi. Wannan lokaci Allah ya ce, **"Zan kuma girgiza al'umman duniya duka don dukiyar al'umman duniya ta samu. Zan kuwa cika Haikalin nan da daraja"** (Haggai 2:7). Ga Yesu, ya shiga cikin Haikali, ya kuma ce jikinsa haikalin Allah ne!

**"Domin a cikinsa ne cikin jiki dukkan cikar allahntaka ke tabbata"** (Kolosiyawa 2:9).


**"...An bayyana shi da jiki..."** (1 Timoti 3:16).


**"Ga shi, budurwa za ta yi juna biyu, ta haifi ɗa, za a kuma sa masa suna Immanuwel." (Ma'anar Immanuwel kuwa, Allah na tare da mu)** (Matiyu 1:23).

**"A cikin masu mulkin zamanin nan ba wanda ya gane hikiman nan, don da sun gane ta, da ba su gicciye Ubangiji Maɗaukaki ba"** (1 Korantiyawa 2:8).

Ka tuna yadda Yesu ya fara bayyana ɗaukakarsa cikin Labari na 4 (Yahaya 2:11). Shugabannin Yahudawa ba su sani Ubangiji mai daraja yana tsakaninsu, yana zamna cikin jikin Yesu, daidai ne ya tsarkake haikalinsa ba, Jikunanmu haikalinsa ne!

## Ina Haikalin Allah Yake Yau?





**"Ashe, ba ku sani ku haikalin Allah ne ba, Ruhun Allah kuma na zaune a zuciyarku?"** (1 Korantiyawa 3:16).

Yesu Almasihu yana zamne a zuciyar kowane mutum wanda ya karɓe shi da gaskiya, ta wurin Ruhu Mai Tsarki! Jikunanmu haikalinsa ne! Abin mamaki! **"Ashe, ba ku sani ba, jikinku haikali ne na Ruhu Mai Tsarki wanda ke zuciyarku, wanda kuka samu a gun Allah? Ai, ku ba mallakar kanku ba ne. Sayenku aka yi da tamani. To, sai ku ɗaukaka Allah da jikinku"** (1 Korantiyawa 6:19-20).

Muhimman abu ne mu yi rayuwarmu na tsarki! Bai kamata mu taɓa yin zunubi da jikunanmu ba, domin idan mun karɓi Yesu cikin zuciyarmu, mun zama haɗe da shi, don haka ya kamata mu yi aminci da shi. Daidai ne ya tsarkake haikalinsa. Daidai ne ya tsarkake kome daga cikinmu wanda bai ji daɗi da shi ba. Bari mu yarda da tsarkakewarsa. Yakan tsarkake mu ta wurin maganarsa.

**"Kaƙa saurayi zai kiyaye ransa da tsarki? Sai ta wurin biyayya da umarnanka"** (Zabura 119:9).

**"In kuwa muka bayyana zunubanmu, to, shi mai alkawari ne, mai adalci kuma, zai kuwa gafarta mana zunubanmu, ya tsarkake mu daga dukkan rashin adalci"** (1 Yahaya 1:9).

**"In kuwa muna zaune a haske** [na maganarsa] **kamar yadda shi yake cikin haske, muna tarayya da juna ke nan, jinin Yesu Ɗansa kuma yana tsarkake mu daga dukkan zunubi"** (1 Yahaya 1:7).


Allah bai kan mai da kowane mai bi haikalinsa ba kaɗai, amma an ce da dukan masu bi jikin Almasihu ne. **"Haka mu ma, ko da ya ke muna da yawa, jiki ɗaya muke"** (Romawa 12:5a). **"Shi ne kai ga jikin nan, wato ikilisiya"** (Kolosiyawa 1:18a).

**"Almasihu Yesu kansa kuwa shi ne mafificin dutsen ginin, dukan wanda aka haɗa tsarin ginin a cikinsa, yana kuma tashi ya zama haikali tsattsarka na Ubangiji. Cikinsa ne ku kuma aka gina ku, ku zama mazaunin Allah ta wurin Ruhu"** (Afisawa 2:20b-22). Kowane mutum inda Allah yake zamne mai daraja ne! Dole ne mu nuna ma masu bi duka ƙamna, da tausayi. Yadda muke yi masu, haka muke yi ga Almasihu.

Bari mu faɗi yadda Bulus ya yi, **"A girmama Almasihu a jikina, ko ta rayuwata, ko ta mutuwata"** (Filibiyawa 1:20b).

Bari mu tabata jikunanmu (haikalin Allah) su zama wurin addu'a inda mu kan yi magana da Allah kowace rana, mu sani yana tare da mu. Kada mu taɓa yarda mu zama kogon barayi inda jin daɗin duniya da dawainiyar duniya su ƙore darajar Allah daga cikinmu.

# LABARI NA 6. YESU YA BAYYANA MA WANI SHUGABAN YAHUDAWA BATUN SABON HAIFUWA



Yahaya 3:1-8, 14-21, 36
1To, akwai wani Bafarisiye,
wai shi Nikodimu, wani shuga-
ban Yahudawa. 2Wannan mu-
tum ya zo wurin Yesu da dad
dare, ya ce masa, "Ya Shuga-
ba, mun sani kai malami ne da
ka zo daga wurin Allah, domin
ba mai iya yin waɗannan mu'-
ujizan da kake yi, sai ko Allah
na tare da shi." 3Yesu ya am-
sa masa ya ce, "Lalle hakika,
ina gaya maka, in ba a sāke
haifar mutum ba, ba zai iya
ganin Mulkin Allah ba." 4Ni-
kodimu ya ce masa, "Kaƙa za a
haifi mutum bayan ya tsufa?
Wato ya iya komawa cikin uwa
tasa ta sāke haifo shi?" 5Yesu
ya amsa masa ya ce, "Lalle ha-
kika, ina gaya maka, in ba an
haifi mutum ta ruwa da ta Ru-
hu ba, ba zai iya shiga Mulkin
Allah ba. 6Abin da mutum ya
haifa mutum ne, abin kuma da
Ruhu ya haifa ruhu ne. 7Kada
ka yi mamaki domin na ce
maka, 'Dole a sāke haifarku.'
8Iska na busawa inda ta ga da-
ma. Kakan ji motsinta, amma
ba ka san inda ta fito ba, da
inda za ta. Haka fa yake ga
duk wanda Ruhu ya haifa."
14"Kamar yadda Musa ya ɗa-
ga macijin nan a jeji, haka ku-
ma dole ne a ɗaga Ɗan Mutum,
15domin duk wanda ya gaskata
da shi, ya sami rai madawwa-
mi.
16"Saboda ƙaunar da Allah ya
yi wa duniya har ya ba da ma-
kaɗaicin Ɗansa, domin duk
wanda ya gaskata da shi kada
ya halaka, sai dai ya sami rai
madawwami. 17Gama Allah bai
aiko Ɗansa duniya yǎ yanke
mata hukunci ba, sai dai do-
min duniya ta sami ceto ta wu-
rinsa.
18"Duk wanda ya gaskata da
shi, ba za a yi masa hukunci
ba. Wanda kuwa bai ba da gas-
kiya ba, an riga an yi masa
hukunci, domin bai gaskata da

sunan makaɗaicin Ɗan Allah ba. [19]Hukuncin kuwa shi ne, haske ya shigo duniya, amma mutane suka fi ƙaunar duhu da hasken, don ayyukansu mugaye ne. [20]Duk mai yin rashin gaskiya yakan ƙi hasken, ba ya kuma zuwa wajen hasken, don kada ayyukansa su tonu. [21]Mai aikata gaskiya kuwa yakan zo wajen hasken, domin a bayyana ayyukansa, cewa da taimakon Allah ne aka yi su."

[36]"Wanda ya gaskata da Ɗan, yana da rai madawwami. Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi."

## Abin da za ka Yi

A. Ka cika filayen da kalma daga cikin labari waɗanda ke daidai.

1. Nikodimu, wani______________Yahudawa (1). Ya zo wurin Yesu______________(2).

[Yesu yana kula da kowane mutum–ko shi mai arziki ne, ko matalauta ne, ko mai ilmi ne, ko mara ilmi ne.]

2. Nikodimu ya yi tsammani Yesu ne______________wanda ya zo daga wurin Allah (2).

3. Yesu ya ce in mutum ya ko ga mulkin Allah sai a________________________mutum (3).

4. Mutum bai iya shiga Mulkin Allah sai an haifi mutum da ta______________da ta______________ba (5).

[Ga Nikodimu, haifuwa ta ruwa ya nuna tsarkakewa. Cikin labari na 2, mun gani Yahaya Maibaftisma ya yi baftisma da ruwa sa'ad da wani ya yi tuba, ya rabu da zunubansa. Yesu ya zo domin ya yi musu baftisma da Ruhu, ya ba mutane sabon rai. Domin mu shiga Mulkin Allah, dole ne mu yarda mu rabu da zunubanmu, mu karɓi rai madawwamiya cikin zukatanmu.]

5. Abin da aka haifa ta wurin mutum______________ne (6).

[Wannan bai nufi jikunanmu kawai ba, amma da duk halin mutum da kwaɗayinsa (Romawa 8:8, 9).]

6. Abin da aka haifa ta wurin Ruhu______________ne (6).

[Sa'ad da iyayenmu nan duniya suka haife mu, suka haife mu da jikuna irin nasu. Sa'ad da an haife mu da Ruhu mai rai, mu kuma muna da rai irin nasa, mun iya fahimci abubuwa na Allah (1 Korantiyawa 2:12, 14).]

7. Dole ne a ɗaga (gicciye) Ɗan Mutum kamar yadda__________ __________ya ɗaga__________________cikin jeji (14).

8. Abin da ya sa Yesu ya zo duniya shi ne domin Allah ya ______________duniya. Duk wanda ya gaskata shi ba zai______________sai dai ya sami________________(16).

9. Allah bai aiko Ɗansa cikin duniya ya________________ (ko da shi ke zai hukumta duniya wata ran); ya aiko Ɗansa don duniya ta____________(17).

10. Duk wanda ya gaskata da shi, ba________________. Za a yi wa mutum hukumci domin bai________________ da sunan makaɗaicin Ɗan Allah ba.

11. Haske ya shigo duniya, amma mutane sun fi ƙaunar_____ __________da__________, domin ayyukansu__________ __________ne. Yesu ya ce da wannan h______________(19). [Ana nufin hukumci ɗin, shi ne rabuwa da Allah har abada ne.]

12.________________________yakan zo wurin haske (21).

[Ba shi ne mutum da yakan aikita ayyuka masu kyau wanda yakan zo wurin haske ba. **"Babu wani mai aiki nagari, babu kam, ko da guda ɗaya"** (Romawa 3:12b). Mutum wanda ya aikata gaskiya shi ne mutumin wanda ya faɗi zunubansa, ya rabu da su, ya karɓi tsarkakewar Ruhu. **"In kuwa muka bayyana zunubanmu, to, shi mai alkawari ne, mai adalci kuma, zai kuwa gafarta mana zunubanmu, ya tsarkake mu daga dukkan rashin adalci"** (1 Yahaya 1:9).]

B. Ka haddace waɗannan ayoyi:

**Yahaya 3:16; Yahaya 3:36.**

## Ina Ma'anar Sabon Haifuwa Ko Sāke Haifuwa

Sabon haifuwa, ko sāke haifuwa, ya nufa a haifi wani "daga bisa," a fara wata rayuwa, ko a fara da wani rai dabam. Haifuwa na duniyan nan yakan mai da mu ɗaya cikin iyalin inda aka haife mu. Sabon haifuwa yakan mai da mu ɗaya cikin iyalin Allah. Ruhu yakan yi aikinsa a cikinmu, mu kan ga sākewa cikin abin da muke yi. Ga misali, mutum wanda ya yi sata ba zai ƙara yi sata ba. Ya zama kamar yadda iska yake busawa. Ba mu iya ga iska ba, amma mukan ga abin da iska ta yi.

Mutum wanda ba a sāke haifuwarsa ba, matacce ne cikin ruhunsa (Afisawa 2:1, 5). A kan wanke zunubanmu ta wurin mutuwar Yesu Almasihu, kuma tsohon al'amurinmu sun shuɗe. Sa'an nan Ruhun Allah yakan rayad da mu da sabon rai–rai na Almasihu. Mun zama sabon halitta. Muna da sabon rai sa'ad da Ruhu Mai Tsarki (Ruhun Yesu da kansa) ya shiga zukatanmu, ya zauna cikinmu. **"Duk wanda ba shi da Ruhun Almasihu kuwa, ba na Almasihu ba ne"** (Romawa 8:9b).

Mun zama masu tarayya da Allah wajen ɗabi'arsa (2 Bitrus 1:4). Muna da sabon nufi. Muna da fahimi domin mu gane maganarsa.

Kai, kamar Nikodimu kake? Kila kai ka zama mai addini, ko mutumin da yakan kiyaye dokoki. Kila kai wani shugaba ne. Ka taɓa samun sabon haifuwa ta wurin Ruhun Allah, domin ka zama sabuwar halitta cikinsa? **"Saboda haka, duk wanda ke na Almasihu, sabuwar halitta ne, tsohon al'amari duk ya shuɗe, ga shi, kome ya zama sabo"** (2 Korantiyawa 5:17). Idan ba a sāke haifuwarka, me ya sa ba ka zo wurin Yesu yanzu, kamar Nikodimu ya yi? Ka roƙi Yesu ya shigo zuciyarka, ya maishe ka sabuwar halitta, ka zama ɗaya cikin iyalin Allah. **"Duk wanda ke da Ɗan, yana da rai. Wanda ba shi da Ɗan Allah kuwa, ba shi da rai"** (1 Yahaya 5:12).

## Musa Cikin Jeji

Da daɗewa, sa'ad da 'ya'yan Isra'ila suke tafiya cikin jeji, Musa yana shugabance su, suka yi gunaguni da baƙar magana akan Allah da Musa. Suka yi gunaguni akan yadda Allah yake lura da su. Sai Ubangiji ya aiko macizai masu zafin dafi a cikin jama'a



su sassari su. Mutane dayawa suka mutu. Jama'a suka zo wurin Musa, suka faɗi zunubansu. Suka roƙi Musa shi yi addu'a ga Allah, ko zai yarda ya kawar masu da macizan. Allah ya ji addu'arsa, ya bada amsa, amma kila ba kamar suka yi tsammani zai yi ba. Ya gaya wa Musa shi ƙera maciji da tagulla, shi sarƙafe shi bisa dirka. Duk wanda maciji ya sara, idan ya dubi maciji na tagulla, zai rayu (Littafin Kidaya 21:4-9).

Zunubi shi ne kamar saren maciji mai mugun dafi. Mu, kuma, za mu mutu sai dai mu dubi Yesu, wanda ya ɗauke zunubinmu (ko shi da kansa bai taɓa yi zunubi ba). Su mutane dayawa suka mutu a jeji. Sai su waɗanda suka dubi macijin suka rayu. Yesu ya faɗakadda Nikodimu shi kuma zai hallaka in bai karɓi sabon rai wurin Yesu ba.

Kamar yadda mutane cikin jeji suka dubi maciji na tagulla mara rai, suka yi rai. Su kuma wajib ne su dubi wanda ya dauƙi zunuban duniya akansa, ya mutu a gicciye (Yahaya 12:32, 33). Duba ka yi rai! Ba wajib ne su fahimta "ta yaya" suka warke da sun dubi macijin nan ba. Sai su yi biyayya da bangaskiya, su duba, su yi rai. Haka kuwa ya zama.


**Ku yi rai... har abada...!**
**Duban Yesu, shi ne rai.**
**Sai ku duba, ku yi rai, Halleluya**
**I, alkawari na Allah ne.**


## Zuwa Wurin Haske

Lokacin da muka zo wurin Yesu, a kan tone zunubanmu domin Yesu haske mai gaskiya ne (Yahaya 1:9). Duhu yakan ɓoye gaskiya, amma haske yakan bayyana ayyuka.

Wanda bai zo wurin hasken Allah ba, ya yi zaɓi ya riƙe zunubansa, bai yarda Allah ya sāke shi ba. Mutum mai zunubi yana kan hanya zuwa hallaka, wurin hukumci. Yana bukata Yesu ya cece shi. Su waɗanda ba su gaskata Ɗan ba, fushin Allah yake bisansu zamne (Yahaya 3:36). Amma waɗanda suka karɓi Yesu, suka shiga sabon rai irin da Yesu yake da shi a sama—rai madawwamiya. **"Wannan shi ne jawabin da muka ji a gunsa, muke kuma sanar da ku cewa Allah haske ne, ba kuwa duhu gare shi ko kaɗan. In mun ce muna tarayya da shi, alhali kuwa muna zaune a duhu, mun yi ƙarya ke nan, ba ma aikata gaskiya. In kuwa muna zaune a haske kamar yadda shi yake cikin haske, muna tarayya da juna ke nan, jinin Yesu Ɗansa kuma yana tsarkake mu daga dukkan zunubi"** (1 Yahaya 1:5-7).

Sa'ad da mutum yake so ya zama mai tsarki, shi zai yarda a tone zunubansa a gafarta masa su. Zaɓen da kake yi ya zama zaɓen rai ko mutuwa. Inda za ka zama har abada ya dangana akan abin da kake yi da Almasihu yanzu. Inda za ka zama har abada ya dangana akan abin da kake yi da haske da kake da shi. Ka kan zo ga hasken? Ko kake ɓoye daga hasken?






**BANGASKIYA + KALMAR ALLAH (YESU) = RAI MADAWWAMI**

# LABARI NA 7. YESU YA MIKA RUWA MAI RAI



Yahaya 4:5-42
5Sai ya zo wani gari na ƙasar
Samariya, wai shi Saikar, kusa
da yankin ƙasar da Yakubu ya
ba ɗansa Yusufu. 6Rijiyar Ya-
kubu kuwa a nan take. Saboda
gajiyar tafiya fa, sai Yesu ya
zauna hakanan a bakin rijiyar.
Wajen tsakiyar rana ce kuwa.
7Sai ga wata Basamariya ta zo
ɗiban ruwa. Yesu ya ce mata,
"Sa mini ruwa in sha." 8Alma-
jiransa kuwa sun shiga gari sa-
yen abinci. 9Sai Basamariyar ta
ce masa, "Ƙaƙa kai Bayahude
za ka roƙe ni ruwan sha, ni da
nake Basamariya?" (Don Ya-
hudawa ba sa cuɗanya da Sa-
mariyawa). 10Yesu ya amsa
mata ya ce, "Da kin san kyau-
tar Allah, da kuma wanda ya
ce miki, 'Sa mini ruwa in sha,'
ai, da kin roƙe shi, shi kuwa
zai ba ki ruwan rai." 11Sai ma-
tar ta ce masa, "Ya Shugaba,
ai, ba ka da guga, rijiyar kuwa
da zurfi. To, ina ka sami ru-
wan nan na rai? 12Ashe, ka fi
ubanmu Yakubu ne, wanda ya
bar mana rijiyar, har shi da
kansa, da 'yayansa, da dab-
bobinsa, suka sha ruwanta?"
13Yesu ya amsa mata ya ce,
"Duk mai shan ruwan nan zai
sāke jin ƙishirwa. 14Amma duk
wanda ya sha ruwan da zan ba
shi, ba zai ƙara jin ƙishirwa ba
har abada. Ruwan da zan ba
shi kuwa zai zama maɓuɓɓuga
a gare shi, yana ɓuɓɓugowa
har ya zuwa rai madawwami."
15Matar ta ce masa, "Ya Shu-
gaba, ka ba ni ruwan nan, don
kada in ƙara jin ƙishirwa, kada
kuma in riƙa zuwa har nan in
ɗiba." 16Sai Yesu ya ce mata,
"Je ki, ku zo da mijinki." 17Sai
matar ta amsa ta ce, "Ai, ba ni
da miji." Yesu ya ce mata,
"Gaskiyarki da kika ce ba ki
da miji, 18don kin auri maza
biyar, wanda kuke tare yanzu
kuwa ba mijinki ba ne. A nan
kam kin yi gaskiya." 19Matar
ta ce masa, "Ya Shugaba, na
dai gane kai annabi ne. 20Ka-

kanninmu sun yi sujada a dut-
sen nan. Ku kuwa kun ce a
Urushalima ne wurin da ya
wajaba a yi sujada yake." [21]Sai
Yesu ya ce mata, "Uwargida,
ki gaskata ni, lokaci na zuwa
da ba za ku yi wa Uba sujada
ba, ko a kan dutsen nan, ko a
Urushalima. [22]Ku kuna yi wa
abin da ba ku sani ba sujada,
mu kuwa muna yi wa abin da
muka sani sujada, domin ceto
ta hanyar Yahudawa yake.
[23]Amma lokaci na zuwa, har
ma ya yi, da masu sujada na
gaskiya za su yi wa Uba sujada
a ruhu, da gaskiya kuma. Lalle
kuwa irin waɗannan masu yi
masa sujada Uba ke nema.
[24]Allah Ruhu ne, masu yi masa
sujada kuwa lalle su yi masa
sujada a ruhu, da gaskiya ku-
ma." [25]Sai matar ta ce masa,
"Na san Masihi na zuwa, wan-
da ake kira Almasihu. Sa'ad
da ya zo kuwa, zai sanar da
mu kome." [26]Yesu ya ce mata,
"Ni ne, ni mai maganan nan
da ke."

[27]Nan take almajiransa suka
dawo, suka yi mamakin ganin
yana magana da mace. Amma
kuwa ba wanda ya ce, "Me ki-
ke bukata?" ko, "Don me kake
magana da ita?" [28]Sai matar ta
bar tulunta, ta koma gari, ta
ce wa mutane, [29]"Ku zo, ku ga
mutumin da ya gaya mini duk
abin da na taɓa yi! Shin, ko
wannan shi ne Almasihu?"
[30]Sai suka fito daga garin suka
nufo shi.

[31]Ana cikin haka sai almaji-
ran suka roƙe shi suka ce, "Ya
Shugaba, ci abinci." [32]Amma
ya ce musu, "Ina da abincin da
ba ku sani ba." [33]Almajiran su-
ka ce wa juna, "Shin, wani ya
kawo masa abinci ne?" [34]Sai
Yesu ya ce musu, "Abincina
shi ne in aikata nufin wanda
ya aiko ni, in kuma cika aikin-
sa. [35]Ba kuna cewa kaka saura
wata huɗu ba? Ina gaya muku
fa, ku ɗaga kai, ku dubi gona-
ki, sun nuna sun isa girbi.
[36]Mai girbi na samun lada,
yana kuma tara amfani zuwa
rai madawwami, domin mai
shuka da mai girbi su yi farin
ciki tare. [37]A nan kam, karin
maganan nan gaskiya ne cewa,
'Wani da shuka, wani da gir-
bi.' [38]Na aike ku girbin abin da
ba ku yi wahalarsa ba. Waɗan-



su sun yi wahala, ku kuwa kun
mori wahalarsu."
39Samariyawa da yawa na
wannan gari suka gaskata da
shi saboda maganar matan nan
da ta ce, "Ya gaya mini duk
abin da na taɓa yi." 40Da Sa-
mariyawa suka iso wurinsa, su-
ka roƙe shi ya sauka a wurin-
su. Ya kuwa kwana biyu a nan.
41Waɗansu kuma da yawa fiye
da na dā, suka ba da gaskiya
saboda magana tasa. 42Sa'an
nan suka ce wa matar, "Yanzu
kam, mun ba da gaskiya, ba
don abin da kika faɗa kawai ba,
domin mu ma mun ji da kan-
mu, mun kuma tabbata lalle
wannan shi ne Mai Ceton duni-
ya."

## Abin da za ka Yi

A. Bada amsoshi daga cikin labarin da ka karanta.

1. Ina abin da ya nuna mana mutumcin Yesu? (6)________

________

2. Me Yesu ya ce wa macen na Samariya? (7)________

________

3. Me ya sa ta yi mamaki da Yesu ya yi magana da ita? (9)____

________

[Su Samariyawa 'ya'yan Yahudawa ne, waɗanda suka yi aure da baƙi na wata kabila. Su ba su yi sujada ga Allah na Yahudawa kaɗai ba, amma suke bauta wa waɗansu alolli kuma. Sa'ad da Yahudawa suka sake gina Haikali a Urushalima ba su yarda Samariyawa su taimake su ba. Amma Yesu yana son kowa da kowa da bukatarsu, ko da shi ke mazajen Yahudawa sun ƙi yarda su yi magana da mace da ke waje.]

4. Me Yesu zai ba macen nan da, ta roƙe shi? (10)________

________

5. Ina bambamcin ko ta sha ruwa daga rigiya ko ta sha ruwan da Yesu ya ce zai ba ta? (13, 14)________

________

________

6. Me Yesu ya sani batun macen nan? (18)__________

____________________

____________________

[Yesu ya san dukan asiran mu, da zunubanmu da muka ɓoye.]

7. Sa'ad da Yesu ya nuna mata zunubanta, me macen ta fara ambata? (20) Ta yi magana batun wurin da ya kamata a yi____

__________.

[Samariyawa suka yi sujada a Mt. Gerizim inda suke da haikali na kansu. Sun yarda da litattafin Musa a Tsohon Alkawari kaɗai. Kai fa, ka fi so ka yi taɗi akan addini maimakon ka yi shiri da Allah?]

8. Yaya masujada na gaskiya suke yi wa Allah sujada? (23)

____________________

[Domin a yi wa Allah sujada na gaskiya, dole ne muna da sabon haifuwa.]

9. Sa'ad da macen nan ta gane Yesu wanene ne, me ta yi? (28, 29)__________

____________________

10. Me ya sa Yesu ya yi ƙoshi sai ka ce ya ƙoshi da abinci. (34)__________

____________________

11. Su Samariyawa suka gaskata Yesu shi wanene ne? (42)__________

B. Haddace: **Yahaya 4:24.**

## Yadda Bangaskiya Ta Kan Yi Girma

Ba ya zama abin mamaki ne yadda macen nan ta ƙaru da sanin Yesu da yadda bangaskiyarta ta ƙaru, da Yesu ya yi magana da ita ba? **Duba aya ta 9.** Da fari, ta sani shi Ba Yahudi ne wanda ya yi mata magana da tawali'u. **Duba aya ta 11.** Ta ƙara ba shi girma da ta ce da shi "Ya Shugaba." **Duba aya ta 19.** Yesu ya san labarinta, sai ta yi tsammani shi annabi ne. **Duba aya ta 29.** Sa'an nan ta fara gaskata shi Almasihu ne.

In mun yarda Yesu ya yi ta yi magana da mu ta wurin Littafi Mai Tsarki, bangaskiyarmu cikinsa za ta ƙaru kuma. **"Ashe, bangaskiya ta wurin jawabin da ake ji take samuwa, jawabin da ake ji kuma ta Maganar Almasihu yake"** (Romawa 10:17).

## Menene Ruwan Rai?

Mace na Samariya ta yi tsammani lalle zai yi kyau im ba dole ta sauƙad da guganta cikin rijiya na Yakubu ba. Zurfin rijiyan nan wajen kafa tassa'in ne. Amma Yesu bai yi magana batun ruwa na rijiya ɗin nan ba. Shi yana yin magana batun jin daɗin da za ta ji a zuciyarta in ta bar neman abubuwan duniya. Ruwan rai da yake ambato, kyauta na rai madawwamiya ce–rai irin da shi kansa yake da shi. Ruwan da zai ba ta, zai zama maɓuɓɓuga a cikinta, zai ɓuɓɓugowa har ya kawo murna da farin ciki da salama sa'ad da ta cika da Ruhu Mai Tsarki.

Macen tana son ruwan, amma da fari, dole Yesu ya kaɗa ita akan zunubanta. Dole ta faɗi zunubanta, ta yarda ta juyo, ta bar su, kafin ta iya karɓa ruwan rai daga wurin Yesu.

## Abin Da Labarin Nan Ya Koya Mana Batun Yin Aikin Allah

1. Kowa yana bukata ya ji Bishara, ya gaskata ga Yesu domin cetonsa. Bai kamata mu ƙi kowa ba. Yesu bai ƙi kowa ba.

2. Gonakin Allah a duniya sun isa girbi. Ya kamata mu duba, mu ga mutane masu yawa kewaye da mu da suna jin yunwar gaskiya, suna so su karɓe ta.

3. Ya yiwu mutum ɗaya ya shuka iri (ya gaya wa waɗansu labarin Yesu, ya ba su 'yan takardu, ya koya masu Maganar Allah). Wani kuma zai yi girbi (wato, zai bi da wani shi karɓi Yesu). Ya kamata mu yarda mu shuka iri, mu yi girbi kuma cikin gonar Allah. Su da suka yi shuka, da su da suka yi girbi za su yi murna tare.

4. Aikata nufin Allah, da cika aikin da Allah ya ba mu yakan kawo mana ƙoshi fiye da yadda abinci yakan ƙosad da mu.

5. Muhimmin abu ne mu ba abokaninmu labarin Yesu, amma muna bukata mu kawo su gareshi, domin su san shi kuma.



Yahaya 4:46-53
46Sai ya sāke zuwa Kana ta ƙasar Galili, inda ya mai da ruwa ruwan inabi. A Kafarnahum kuwa akwai wani bafada wanda ɗansa ba shi da lafiya.
47Da jin cewa Yesu ya fito ƙasar Yahudiya ya komo ƙasar Galili, sai ya tafi wurinsa, ya roƙe shi ya je ya warkar da ɗansa, don yana bakin mutuwa.
48Yesu ya ce masa, "In ba mu'ujizai da abubuwan al'ajabi kuka gani ba, ba yadda za a yi ku ba da gaskiya."
49Sai bafadan nan ya ce masa, "Ya Shugaba, ka zo tun ƙaramin ɗana bai mutu ba."
50Yesu ya ce masa, "Yi tafiyarka, ɗanka a raye yake." Mutumin kuwa ya gaskata maganar da Yesu ya faɗa masa, ya yi tafiyarsa.
51Yana cikin tafiya sai ga bayinsa sun taryo shi, suka ce masa, "Ɗanka a raye yake."
52Sai ya tambaye su ainihin lokacin da ya fara samun sauƙi. Suka ce masa, "Jiya da ƙarfe ɗaya na yamma zazzaɓin ya sake shi."
53Sai uban ya gane, daidai lokacin nan ne, Yesu ya ce masa, "Ɗanka a raye yake." Shi da kansa kuwa ya ba da gaskiya, da jama'ar gidansa duka.

## Ikon Maganar Allah

Sa'ad da Allah ya yi magana, wani abu yakan faru! Allah wanda ya halicci duniya da abin da ke cikinta ta wurin yin magana, yana magana da bafada, ya ce, "Yi tafiyarka, ɗanka a raye yake." Haka ma ya zama.

Yesu ya ce duk abin da aka alkawarta cikin Littafi Mai Tsarki zai faru (Matiyu 5:18). Ka gaskata Maganar Allah? Ta wurin abin da kake yi, ya nuna lalle ka gaskata shi–kamar mutumin cikin labarin nan?

Maganarmu suna da iko kuma, in Yesu yake zamne a zuciyarmu. Cikin Markus 11:22, 23 Yesu ya ce wa almajiransa, "**Yesu ya amsa musu ya ce, 'Ku gaskata da Allah. Hakika, ina gaya**

**muku, kowa ya ce wa dutsen nan, 'Ka ciru, ka faɗa teku,' bai kuwa yi shakka a zuciyarsa ba, amma ya gaskata abin da ya faɗa zai auku, sai a yi masa shi."** Maganganunmu da muka faɗi tare da bangaskiya suna da iko. Wane irin magana kake yi?" Kana magana na ƙarfafa juna, ko irin na yin ta'aziya, ko irin ƙamna?

## Abin Da Labarin Ya Koya Mana Batun Addu'a

Yesu yakan amsa addu'armu yau? Ibraniyawa 13:8 ya gaya mana cewa Yesu ba ya sakewa, **"shi ne a jiya, da yau, hakika har abada ma."** Mun sani wajib ne mu kawo masa bukatarmu. Ya ce, **"Wanda ya zo gare ni ba zan kore shi ba ko kaɗan** (Yahaya 6:37). Kuma ya ce, **"Ku yi ta roƙo, za a ba ku. Ku yi ta nema, za ku samu. Ku yi ta ƙwanƙwasa, za a kuwa buɗe muku"** (Matiyu 7:7).


Sa'an nan, dole ne mu zo da bangaskiya, mu gaskata lalle zai ba mu amsa. **"In ba game da bangaskiya ba kuwa, ba shi yiwuwa a faranta masa rai. Domin duk wanda zai kusaci Allah, lalle ne ya gaskata, akwai shi, yana kuma sakamako ga masu nemansa"** (Ibraniyawa 11:6).

Wajib ne mu karɓi amsa wanda ya ba mu. Bafada ya roƙi Yesu ya zo gidansa amma Yesu bai yi haka ba. Maimakon haka, ya ce, "Yi tafiyarka, ɗanka a raye yake." Kila ba zai ba ka amsa daidai da kake tsammani ba, amma zai yi abin da ya fi maka kyau, kowane lokaci kuwa zai yi daidai da Maganarsa.

Bangaskiya ba zai tsirad da kai kowane lokaci ba. (Ka bincike Ibraniyawa 11:35-39) amma zai kawo bishewa da salama. **"Kada ku damu da kome, sai dai a kowane hali ku sanar da Allah bukatunku, ta yin addu'a da roƙo, tare da gode wa Allah. Ta haka salamar Allah, wadda ta fi gaban dukkan fahimta, za ta tsai da zukatanku da tunaninku ga Almasihu Yesu"** (Filibiyawa 4:6, 7).

Sa'ad da ka gaskata Allah, Allah ya yi aikinsa da iko, zai ƙarfafa bangaskiyarka. Zai ƙarfafa bangaskiyar iyalin gidanka kuma, kamar yadda jama'ar gidan bafadan suka ba da gaskiya.

# LABARI NA 9. YESU YA WARKAD DA MARASA LAFIYA



Yahaya 5:1-9, 14-18
[1]Bayan haka aka yi wani idi
na Yahudawa, Yesu kuwa ya
tafi Urushalima. [2]A Urushali-
ma, kusa da Kofar Tumaki,
akwai wani ruwa da ake ce da
shi Betasda da Yahudanci, an
kuwa kewaye shi da shirayi
biyar. [3]A shirayin nan kuwa
marasa lafiya da yawa sun sa-
ba kwanciya, makafi, da gura-
gu, da shanyayyu. [Suna jira a
motsa ruwan. [4]Don lokaci loka-
ci wani mala'ika yakan sauko
cikin ruwan ya motsa shi. Duk
kuwa wanda ya fara shiga ba-
yan an motsa ruwan, sai ya
warke duk irin cutar da yake
da ita.] [5]A nan kuwa akwai
wani mutum da ya shekara ta-
latin da takwas da rashin lafi-
ya. [6]Da Yesu ya gan shi kwan-
ce, ya kuma sani ya daɗe da
wannan hali, sai ya ce masa,
"Kana so a warkar da kai?"
[7]Marar lafiyar ya amsa masa
ya ce, "Ya Shugaba, ai, ba ni
da wanda zai angaza ni cikin
ruwan lokacin da aka motsa
shi. Lokacin da na doshi ru-
wan kuma sai wani ya riga ni
shiga." [8]Sai Yesu ya ce masa,
"Tashi, ka ɗauki shimfiɗarka,
ka yi tafiya!" [9]Nan take mutum-
in ya warke, ya ɗauki shimfi-
ɗarsa ya yi tafiya. Ran nan ku-
wa Asabar ce.

[14]Bayan haka Yesu ya same shi
a Haikali, ya ce masa, "Ka ga
fa, ka warke! To, ka daina yin
zunubi, don kada wani abu da
ya fi wannan muni ya same ka."
[15]Sai mutumin ya tafi ya gaya
wa Yahudawa, Yesu ne ya war-
kar da shi. [16]Saboda haka Yahu-
dawa suka fara tsananta wa Ye-
su, wai don yana yin irin waɗan-
nan abubuwa ran Asabar.

[17]Yesu kuwa ya amsa musu
ya ce. "Ubana na aiki har yan-
zu, ni ma ina yi." [18]Don haka
Yahudawa suka ƙara nema su
kashe shi, ba wai don ya keta
Asabar kaɗai ba, har ma do-
min ya ce Allah Ubansa ne,
wato yana daidaita kansa da
Allah.

## Abin da za ka Yi

Ka cika filayen nan.

1. Wani mutum yana jira a gefen Betasda. Yana da rashin lafiya, ba shi da ƙarfin jiki shekara______________________ (5).
2. Yesu ya tambaye shi wata muhimman tambaya: "Kana so a______________________da kai?" (6)
3. Yesu ya gaya masa shi yi abin da mutumin ya gane bai yiwuwa. Ya ce, "______________________shimfiɗarka, ka yi______________________(8).
4. Daga baya, lokacin da Yesu ya same shi a Haikali, ya ce, "Ka ga fa, ka warke! To,______________________don kada wani abu da ya fi wannan muni ya same ka" (14).
5. Yahudawa suka nema, su kashe Yesu saboda dalilai guda biyu: (a) domin ya______________________(18) [Ya warkadda mutumin a ran Asabar lokacin da bai daidai Yahudawa su yi aiki ba], (b) Ya ce kuma Allah______________________wato ya mai da kansa daidai da Allah(18).

## Kai, Kana Bukata A Maishe Ka Lafiya!

Kila kana bukata a maishe ka lafiya, kuma a ƙarfafa jikinka, ko a tunaninka, ko a zuci. Kila kana da al'ada mara kyau wanda ya hana ka, ka bauta wa Allah yadda kake so. Kila kana da ɗacin rai wanda yana ci maka a zuci.

Yesu ya san bukatarka, yana ce maka, **"Kana so a warkar da kai?"** Kila za ka kawo hujoji iri iri, cewa ga dalilan ke nan. Kila kai ɗaya ne cikin iyalinka da ke mai bi, ko a makarantarka. Ko kana tsammani dawainiyarka suke hana ka. Waɗannan ba su da wuya wurin Yesu ba. Ya iya maishe ka lafiyayyu nan da nan. Ya yiwu zai roƙe ka ka yi wani abu wanda ka yi tsammani ba shi yiwuwa, kamar yadda ya roƙi mutumin ɗin wanda bai iya tashi ya yi tafiya ba, ya ɗauki shimfiɗarsa! Komenene da ya roƙe ka, ka yi biyayya, Yesu zai ba ka ikon da ka ke bukata ka yi shi. Zai warkad da kai. Sa'annan zai bishe ka, ka yi rayuwa mai nasara.

# LABARI NA 10. TASHIN MATATTU IRI GUDA BIYU

Yahaya 5:24-29

24 Lalle hakika, ina gaya mu-
ku, duk mai jin maganata, ya-
ke kuma gaskata wanda ya ai-
ko ni, yana da rai madawwa-
mi. Ba za a yi masa hukunci
ba, domin ya riga ya tsere wa
mutuwa, ya kai ga rai. 25 "Lalle
hakika, ina gaya muku, lokaci
na zuwa, har ma ya yi, da ma-
tattu za su ji muryar Ɗan
Allah, masu ji kuwa su rayu.
26 Yadda Uba kansa yake tu-
shen rai, haka ya sa Ɗan ya
zama tushen rai. 27 Ya kuma ba
shi ikon zartar da hukunci, sa-
boda shi Ɗan Mutum ne. 28 Kada
ku yi mamakin wannan, domin
lokaci na zuwa da duk waɗan-
da ke kaburbura za su ji mur-
ya tasa, 29 su kuma fito, wa-
ɗanda suka aikata nagarta su
tashi, tashin rai, waɗanda suka
yi rashin gaskiya kuwa su ta-
shi, tashin hukunci.

## Abin Yin Tunani

Abin mamaki ne muka ji Yesu yana ƙwanƙwasa a ƙofar zuciya. Mua yarda masa ya shiga zuciya, sa'an nan mun tabbata muna da rai madawwani. Mun sani ba za a taɓa yi mana hukunci ba. Mun sani mun riga mun ratsa mutuwa zuwa rai. Kakan yi tunani cewa, yaya wannan ya yiwu? Dalili ke nan, domin Yesu yana da rai cikin kansa (aya ta 26). Su waɗanda ba su da Almasihu ba, ba su iya faranta wa Allah rai ba (Romawa 8:8). Sabili da haka lokacin da an tashe su daga cikin kabari, za a yi masu hukunci, za a raba su da Allah har abada abadin.

## Abin da za ka Yi

Ka haddace Yahaya 5:24 don ya tabbata maka ma'anar cetonka. Idan kana jin Maganar Allah, kana dogara gare shi (biyayya gare shi, ya nuna kana dogara gare shi) kada ka yarda Shaiɗan ya sa shakka a tunaninka. Allah yana son ka sani kai nasa ne. In wani abu ya shiga tsakaninka da Allah, Allah zai nuna maka don ka faɗi zunubinka, ka rabu da shi kuma. Allah zai shirya abin, Shaiɗan yakan kai ƙara kurum.

# LABARI NA 11. YESU GURASAR RAI

Yahaya 6:5-14, 35, 47-51, 53-56, 63

5Da Yesu ya ɗaga kai ya han-
go babban taro na doso shi, sai
ya ce wa Filibus, "Ina za mu
sayo gurasar da mutanen nan
za su ci?" 6Ya faɗi haka ne fa
domin ya gwada shi, saboda shi
kansa ya san abin da zai yi.
7Filibus ya amsa masa ya ce,
"Ai, ko gurasar dinari metan
ma ba ta isa kowannensu ya
sami kaɗan ba." 8Sai ɗaya
daga cikin almajiransa, wai shi
Andarawas, ɗan'uwan Bitrus,
ya ce masa, 9"Ga wani ɗan
yaro nan da gurasa biyar na
sha'ir, da kuma kifi biyu.
Amma me waɗannan za su yi
wa mutane masu yawa haka?"
10Yesu ya ce, "Ku ce wa mu-
tane su zauna." Wuri ne kuwa
mai ciyawa. Sai mazaje suka
zazzauna, su wajen dubu bi-
yar. 11Yesu ya ɗauki gurasar,
bayan ya yi godiya ga Allah
kuma, sai ya rarraba wa wa-
ɗanda ke zazzaune. Haka kuma
ya yi da kifin, gwargwadon abin
da ya ishe su. 12Da suka ci suka
ƙoshi, sai ya ce wa almajiransa,
"Ku tattara gutsattsarin da suka
saura, kada kome ya ɓata."
13Sai suka tattara gutsattsarin
gurasan nan biyar na shar'ir
da suka saura bayan kowa ya
ci, suka cika kwando goma sha
biyu. 14Da jama'a suka ga
mu'ujizar da ya yi, suka ce,
"Lalle, wannan shi ne annabin
nan mai zuwa duniya!"

35Yesu ya ce musu, "Ni ne
Gurasa mai ba da rai. Wanda
ya zo gare ni ba zai ji yunwa
ba har abada, wanda kuma ya
gaskata da ni ba zai ƙara jin
ƙishirwa ba har abada.

47Lalle hakika ina gaya mu-
ku, wanda ya ba da gaskiya,
yana da rai madawwani. 48Ni
ne Gurasa mai ba da rai. 49Ka-
kannin kakanninku sun ci man-
na a jeji, amma kuwa sun mu-
tu. 50Ga Gurasa mai saukowa



daga Sama, domin kowa yǎ ci, kada ya mutu. [52]Ni ne Gurasan rai da ya sauko daga Sama. Kowa ya ci Gurasan nan, zai rayu har abada. Har ma gurasar da zan bayar naman jikina ne, domin duniya ta rayu."

[53]Sai Yesu ya ce musu, "Lalle hakika, ina gaya muku, in ba ku ci naman jikin Ɗan Mutum ba, kuka kuma sha jininsa, ba rai a gare ku. [54]Duk wanda ke cin naman jikina, ya ke kuma shan jinina, yana da rai madawwami, ni kuwa zan tashe shi a ranar ƙarshe. [55]Domin naman jikina abinci ne na hakika, jinina kuma abin sha ne na hakika. [56]Duk wanda ke cin naman jikina, yake kuma shan jinina, a cikina yake zaune, ni kuma a cikinsa.

[63]Ai, Ruhu shi ne mai rayarwa, jiki kam ba ya amfana kome. Kalmomin da na faɗa muku ruhu ne, da kuma rai.

## Abin da za ka Yi

Haddace: **Yahaya 6:35** da **Yahaya 6:63.**

## Abin Da Labarin Ke Koya Mana

1. Yesu yakan kula da bukatarmu. Ya riga ya san yadda zai biya dukan bukatarmu, amma yana son ya gwada bangaskiyarmu cikinsa. Yana so mu dogara gare shi don kowace bukata da muke da shi.

2. Ko Yesu yakan yi godiya don kankannin abin da yake da shi. Allah ya ce mana, **"Ku yi godiya ga Allah a kowane hali, domin shi ne nufin Allah game da ku ta wurin Almasihu Yesu"** (1 Tasalonikawa 5:18).

3. Yesu ya iya biya kowace bukata a yalwace. **"Ɗaukaka tǎ tabbata ga wannan da ke da ikon aikatawa fiye da dukkan abin da za mu roƙa, ko za mu zata nesa, wato aikatawa ta ƙarfin ikonsa da ke aiki a zuciyarmu"** (Afisawa 3:20).

4. Allah ba ya so a ɓatad da abu banza. Yana son a yi amfani da dukan abin da ya ba mu don kada kome ya ɓace.

Yana son mu yi amfani da lokacinmu a hankali. **"Ku yi matuƙar amfani da lokaci don kwanaki mugaye ne. Don haka kada ku zama marasa azanci, sai dai ku fahimci abin da ke nufin Ubangiji"** (Afisawa 5:16, 17).

Yana son mu yi amfani da iyawarmu ko talanti namu da hankali. **"Sai ubangijinsa ya ce masa, 'Madalla, bawan kirki, mai**

**aminci. Kā yi gaskiya a kan ƙaramin abu, zan ɗora ka a kan mai yawa. Ka zo ku yi farin ciki tare da ubangijinka'"** (Matiyu 25:21).

Yesu yana son mu yi amfani da kuɗinmu a hankali. **"Kada ku tara wa kanku dukiya a duniya, inda asu da tsatsa ke ɓatawa, inda ɓarayi kuma ke karyawa su yi sata. Sai dai ku tara wa kanku dukiya a Sama, inda ba asu da tsatsa da za su ɓata, inda kuma ba ɓarayin da za su karya su yi sata. Domin kuwa inda dukiyarka take, a nan zuciyarka ma take"** (Matiyu 6:19-21).

5. Lokacin da almajirai suka karɓi abinci daga wurin Yesu, suka rarraba wa taron masu yunwa. Sa'ad da muka karɓi abinci na ruhaniya daga wurin Yesu kowace rana, muna da abin da za mu rarraba ma su da suke kewaye da mu waɗanda suke bukata gurasa ta rai.

## Gurasa Iri Biyu

Taro mai girma na mutane suka yi murna don abincin da aka ba su, sa'ad da suke da yunwa mai yawa. Suna son Yesu ya zama sarkinsu, don kada su damu akan yin aiki don su sami abinci! Amma Yesu ya tuna masu batun abin da ya faru tun dā da kakaninsu, 'Ya'yan Isra'ila suke tafiya daga ƙasar Masar zuwa ƙasan da Allah ya alkawarta masu. Babban taron suka ji yunwa a jeji. Allah ya aiko masu abinci daga sama, ya ciyad da su kowace rana! Wannan mu'ujiza abin mamaki ne (Fitowa 16:4-35)! Mutanen ba su sani irin abincin nan ba sai suka kira shi manna. Ma'anar manna shi ne "menene wannan?"

Daga baya Allah ya koya wa mutanen dalilin da ya yi haka. Musa ya gaya wa mutane, **"Ku tuna yadda Ubangiji Allahnku ya bishe ku shekarun nan arba'in a jeji don ya koya muku tawali'u. Ya jarraba ku don ya san zuciyarku, ko za ku kiyaye umarnansa ko babu. Ya koya muku tawali'u, ya bar ku da yunwa, ya ciyar da ku da manna wadda ba ku sani ba, kakanninku kuma ba su sani ba, domin ya sa ku sani, ba da abinci kaɗai mutum ke rayuwa ba, amma mutum yana rayuwa da kowane irin abin da yake fitowa daga wurin Ubangiji"** (Maimaitawar Shari'a 8:2, 3).



Ko da shi ke Allah ya ba su manna daga sama don shekaru masu yawa, manna ta zama gurasa domin jikunansu kurum. Mutane da suka ci suka ƙara tsufa, suka mutu. Yanzu, haka yake, sa'ad da Yesu ya ciyad da taron mutane, gurasa da suka ci, ya zama don jikunansu kaɗai kuma. Ko suka ci, suka ƙoshi, suka ƙara tsufa, suka mutu daga baya.

Yesu yana da labari mai kyau dominsu! Yana miƙa masu wani irin abinci, wanda idan suka ci ba za su mutu ba. I, jikunansu za su mutu, amma su da kansu ba za su taɓa mutuwa ba. Yesu Almasihu zai ta da jikunansu kwanakin ƙarshe, sa'ad da ya dawo duniya. Ya gaya wa mutane shi da kansa, wani irin gurasa ne da za a iya ci! Shi ne gurasa ta rai dominsu! Ya sauƙo daga sama kamar yadda manna ya zo daga sama. Ya zo domin ya bada ransa domin duniya. Duk wanda ya ci shi–ko kuwa suka karɓe shi a zuciyarsu–suke da rai irin na Yesu wanda ba zai taɓa mutuwa ba.

Yaya muka iya ci wannan gurasa ta rai–wato Yesu? Yaya muka iya sha jininsa? Muka iya karɓi hadayar Yesu da ya yi a gicciye domin cetonmu. Muka iya karɓe shi Ɗan Rago na Allah wanda jininsa ya rufe zunubanmu. Muka iya karɓi Ruhunsa mai rai, wanda ke ba mu rai cikin zukatanmu. Kuma muka iya karɓi Maganarsa mai rai ta wurin bincikin su, mu yi masa biyayya. Muna bukata mu yi ta ɗiba daga cikin ransa kowace rana, daidai yadda muke bukata mu ci abinci don jikunanmu kowace rana.

**Cikin ruhaniya ka iya ci jikin Yesu, ka sha jininsa kowace rana.**

1. Kowace rana sai ka yi tafiya cikin hasken maganarsa. Idan ka yi zunubi, ka faɗi zunubinka ga Allah, jininsa zai tsarkake ka, domin ka ƙara yi zumunci tare da shi (1 Yahaya 1:7, 9).

2. Kowace rana ka roƙi Yesu ya cika ka da Ruhunsa. Cikin kowane abin da ka ke yi, ka dogara ga ikon Ruhunsa wanda ke cikinka. Ka karɓi koyarwa daga cikin Maganarsa kowace rana. Maganarsa rai ne gare ka. Ka yi addu'a gare shi kowace rana —kai da shi kaɗai. Sa'annan ka yi tunani a kansa, ka yi magana da shi cikin zuciyarka kullum. Za ka gani halinka zai zama kamar nasa.

Allah ya yi maka alkawali mai kyau in ka yi waɗannan abubuwa. **"Sa'an nan mutane waɗanda ke tsoron Ubangiji suka yi magana da junansu, Ubangiji kuwa ya kasa kunne ya ji abin da suke cewa. A gabansa aka rubuta a littafin tarihin waɗanda ke tsoron Ubangiji, suna kuwa girmama shi. "Ni Ubangiji Mai Runduna, na ce, za su zama mutanena na ainihi, a ranar da na aikata. Zan ji ƙansu kamar yadda mahaifi yakan ji ƙan ɗansa wanda ke masa hidima"** (Malakai 3:16, 17).

## Maganar Allah Ita Ce Abinci Mai Ruhaniya Gare Ka

Da daɗewa Ayuba ya ce, **"A kullum ina aikata abin da Allah ya umarta, ina bin nufinsa, ba nufin kaina ba"** (Ayuba 23:12).


Irmiya ya faɗi cewa, **"Maganarka da na samu na ci. Maganarka kuwa ta zama abar murna a gare ni, ta faranta mini zuciya. Gama ana kirana da sunanka, ya Ubangiji Allah Mai Runduna"** (Irmiya 15:16).

Marubucin Zabura ya ce, **"Ɗanɗanon ka'idodinka akwai zaƙi, har sun fi zuma zaƙi!"** (Zabura 119:103).

Bitrus ya ƙarfafa cewa, **"Kamar jariri sabon haihuwa, ku yi marmarin shan madara marar gami mai ruhu, domin ku girma da shi, har ya kai ku ga samun ceto, in dai har kun ɗanɗana alherin Ubangiji"** (1 Bitrus 2:2, 3).

Bari mu ci Maganar Allah kowace rana!

## LABARI NA 12. YESU NA TAFIYA KAN RUWAN TEKU



Yahaya 6:16-21
16 Da magariba ta yi, sai al-
majiransa suka gangara teku.
17 Suka shiga jirgi, suka tasar
wa haye tekun zuwa Kafarna-
hum. A sa'an nan duhu ya yi,
Yesu kuwa bai zo wurinsu ba
tukuna, 18 Sai tekun ta fara
hauka saboda wata riƙaƙƙiyar
iska da ke busawa. 19 Bayan sun
yi tuƙi wajen mil uku ko huɗu,
sai suka hango Yesu na tafiya
kan ruwan, ya kusato jirgin.
Sai suka firgita. 20 Amma ya ce
musu, "Ni ne, kada ku ji tso-
ro." 21 Sa'an nan suka yarda su
karɓe shi a jirgin. Nan da nan
sai ga jirgin a gaɓar da za su.

### Abin Yin Tunani

Kana zamanka cikin hadari? Rayuwarka ta zama sai ka ce da duhu yanzu? Sai ka ce Yesu yana da nesa? Ko kai da waɗanda ke tare da kai kuna fama kamar cikin hadari, kuna ƙoƙari da rashin ƙarfin kanku ku kai wancan ketare? In haka ne, sai ku sani Yesu ya kula, ya sani, ya gani. Shi yana zuwa wurinka cikin wahalarka. Kada ka ji tsoro. Ka yarda Yesu ya shiga tare da kai cikin wahalarka. Ka ba shi iznin shirya maka shi. Shi zai kwantadda hadarin, ko wahalan, zai ba ka hanyar tsira, za ka tsira lafiya. **"Ko da hanyan nan ta bi ta tsakiyar duhu na mutuwa, ba zan ji tsoro ba, ya Ubangiji, gama kana tare da ni!"** (Zabura 23:4a).

## LABARI NA 13. YESU YA YI MAGANA BATUN 'YANCI

Yahaya 8:31-37, 42, 47
31 Sai Yesu ya ce wa Yahu-
dawan nan da suka gaskata
shi, "In dai kun zauna kan
maganata, hakika ku almaji-
raina ne. 32 Za ku san gaskiya,
gaskiyar kuwa za ta 'yanta
ku."


33 Suka amsa masa suka ce,
"Ai, mu zuriyar Ibrahim ne,
ba mu taɓa bauta wa kowa
ba. Yaya kuma za ka ce za a
'yanta mu?" 34 Sai Yesu ya am-
sa musu ya ce, "Lalle hakika,
ina gaya muku, duk mai aikata
zunubi bawan zunubi ne. 35 Ai,
bawa ba ya ɗorewa a gida har
abada, ɗa kuwa na ɗorewa. 36 In
kuwa Ɗan ya 'yanta ku, za ku
'yantu, 'yantuwar gaske. 37 Na
san dai ku zuriyar Ibrahim ne,
amma kuwa kuna neman ka-
she ni, don maganata ba ta shi-
garku.

42 Yesu ya ce musu, "Da Allah
ne Ubanku da kun ƙaunace ni,
domin daga wurin Allah na fi-
to, ga ni nan kuwa. Ban zo do-
min kaina ba, shi ne ya aiko
ni.

47 Na Allah yakan saurari
Maganar Allah. Abin da ya sa
ba kwa sauraronta ke nan, don
ku ba na Allah ba ne."

Yahaya 7:17

17 Duk mai son aikata nufin
Allah zai san koyarwan nan ko
ta Allah ce, ko domin kaina
nake faɗa.



## Abin da za ka Yi

Cika filayen:

1. In dai kun__________________, Yesu ya ce, hakika ku __________________(8:31).

2. __________________kuwa za ta 'yanta ku (8:32).

3. Duk mai aikata zunubi__________________ ne (8:34).

4. In kuwa__________________ya 'yanta ku (daga zunubi) za ku 'yantu, 'yantuwar gaske (8:36).

5. Yesu ya ce musu, "Da Allah ne Ubanku, da kun__________ __________ni (8:42).

6. Na__________________yakan saurari Maganar Allah (8:47).

7. Duk mai son aikata__________________Allah zai,__________________ ko ta Allah ce, ko domin kaina nake faɗa (7:17).

# LABARI NA 14. YESU NE HASKEN DUNIYA



Yahaya 8:12
12Sai Yesu ya ƙara musu da cewa, "Ni ne Hasken duniya. Wanda ke bina ba zai yi tafiya a duhu ba, amma zai sami hasken rai."

Yahaya 9:1-9, 13-25, 33-38
1Yesu na wucewa sai ya ga wani mutum da aka haifa makaho. 2Sai almajiransa suka tambaye shi suka ce, "Ya Shugaba, wa ya yi zunubi da aka haifi mutumin nan makaho, shi, ko iyayensa?" 3Yesu ya amsa ya ce, "Ba wai domin mutumin nan ko iyayensa sun yi zunubi ba, sai domin a nuna aikin Allah ne a kansa. 4Lalle ne mu yi aikin wanda ya aiko ni tun da sauran rana. Ai, dare zai yi sa'ad da ba mai iya aiki. 5Muddin ina duniya ni ne hasken duniya." 6Da ya faɗi haka sai ya tofa yau a ƙasa, ya cuɗa ƙasa, ya shafa a idanun makahon, 7ya ce masa, "Je ka, ka wanke ido a ruwan Siluwam," wato aikakke. Shi ke nan sai ya je ya wanke ido, ya komo yana gani. 8Maƙwabta da waɗanda suka saba ganinsa dā yana bara, suka ce, "Ashe, ba wannan ne yakan zauna yana bara ba?" 9Waɗansu suka ce, "Shi ne mana." Waɗansu kuwa suka ce, "A'a, kai dai, sun yi kama." Shi kuwa ya ce, "Sosai ni ne!"

13Sai suka kai wa Farisiyawa mutumin da ke makaho a dā. 14To, ran Asabar ne Yesu ya cuɗa ƙasar ya buɗe masa ido. 15Farisiyawa ma suka tambaye shi ta yadda aka yi ya sami gani. Ya ce musu, "Cuɗaɗɗiyar ƙasa ya shafa a idona, na wanke, ina gani." 16Saboda haka waɗansu Farisiyawa suka ce, "Mutumin nan ba daga Allah yake ba, don ba ya kiyaye Asabar." Waɗansu kuwa suka ce, "Yaya mutum mai zunubi zai iya yin mu'ujizai haka?" Sai rabuwa ta shiga tsakaninsu. 17Sai suka

sāke ce wa makahon, "To, kai fa, me ka gani game da shi, da ya ke kai ya buɗe wa ido?" Ya ce, "Ai, annabi ne." [18]Yahudawa kam, ba su gaskata shi makaho ne a dā ba, ya kuma sami gani, har suka kira iyayen wanda ya sami gani, [19]suka tambaye su suka ce, "Wannan ɗanku ne da kuke cewa an haife shi makaho? To, ta yaya yake iya gani yanzu?" [20]Sai iyaye nasa suka amsa suka ce, "Mun dai san wannan ɗanmu ne, makaho ne aka haife shi. [21]Amma ta yadda aka yi yake gani yanzu ba mu sani ba, ba mu ma san wanda ya buɗe masa idon ba. Ku tambaye shi, ai, ba yaro ba ne, zai faɗa da bakinsa." [22]Iyayensa sun faɗi haka ne don tsoron Yahudawa, don dā ma Yahudawa sun ƙulla, cewa kowa ya amsa, cewa shi ne Almasihu, za a fisshe shi daga jama'a. [23]Shi ya sa iyayensa suka ce, "Ai, ba yaro ba ne, ku tambaye shi." [24]Sai suka sāke kiran mutumin nan da ke makaho a dā, suka ce masa, "Ka tsoraci Allah dai! Mu kam, mun san mutumin nan mai zunubi ne." [25]Sai ya amsa ya ce, "Ko mai zunubi ne, ni ban sani ba. Abu ɗaya kam, na sani, dā ni makaho ne, yanzu kuwa ina gani."

[33]Da mutumin nan ba daga Allah ya fito ba, da ba abin da zai iya yi." [34]Suka amsa masa suka ce, "Kai da aka haifa a baƙin zunubi ne za ka koya mana?" Sai suka kore shi. [35]Yesu ya ji labari sun kore shi. Da ya same shi, ya ce, "Ka gaskata da Ɗan Allah ko?" [36]Ya amsa ya ce, "Wanene shi, ya Shugaba, da zan gaskata da shi?" [37]Yesu ya ce masa, "Ai, ka gan shi, shi ne ma mai magana da kai." [38]Sai ya ce, "Ya Ubangiji, na ba da gaskiya," ya kuma yi masa sujada.

## Wanene Ya Faɗi?

1. Wa ya ce, "Dare zai yi sa'ad da ba mai iya aiki"?________ ____________(Aya ta 4).
2. Wa ya ce, "Ba wannan ne yakan zauna yana bara ba?" ________________(8).
3. Wa ya ce, "Mutumin nan ba daga Allah yake ba"?________ ________________(16). [Farisiyawa waɗansu masu addini ne. Suka ƙarfafa biyayya ga shari'ar Musa da aladunsu.]

4. Wa ya ce, "Ku tambaye shi, ai, ba yaro ba ne, zai faɗa da bakinsa"?____________________(21-23).

[Abin alhali ne a fitar da wani daga jama'a. Za a yi da shi sai ka ce kamar kuturu. Ba za a ci da shi, ko ba za a yi kowane sha'ani da shi ba.]

5. Wa ya ce, "Da mutumin nan ba daga Allah ya fito ba, da ba abin da zai iya yi"?________________ ____________(33).

6. Wa ya ce, "Ka gaskata da Ɗan Allah ko?"____________(35).

7. Wa ya ce, "Ya Ubangiji, na ba da gaskiya"?____________(38).

## Yesu Ya Kawo Haske

Sa'ad da Yesu ya buɗe idanun makaho, ya kawo masa haske a ransa. Amma Yesu ya fi son ya nuna wa mutane ya zo musamman domin ya buɗe idanun zuciyar mutane waɗanda suke zamne cikin duhu.

Shekaru dayawa a dā, Allah ya yi alkawari ga annabawansa, wani zai zo wanda zai kawo haske. Allah ya ambata Yesu: **"Ni Ubangiji, na kira ka, na kuma ba ka iko domin ka ga ana aikata gaskiya a duniya. Ta wurinka zan yi wa dukan mutane alkawari, ta wurinka zan kawo haske ga al'ummai. Za ka buɗe idanun makafi, ka kuma kwance waɗanda ke ɗaure a kurkuku masu duhu."** (Ishaya 42:6, 7). Ishaya ya ga ranar Ubangiji: **"Jama'ar da suka yi tafiya cikin duhu, sun ga babban haske! Suka zauna a inuwar mutuwa, amma yanzu haske ya haskaka su"** (Ishaya 9:2).

Sa'ad da Yesu ya ce shi Hasken duniya ne, Yahudawa sun sani yana ce da kansa Allah, domin Allah haske ne. **"Ubangiji ne haskena da cetona"** (Zabura 27:1a). **"Sa'ad da na zauna cikin duhu, Ubangiji zai haskaka ni"** (Mika 7:8b). Dawuda yana yin godiya ga Ubangiji da ya ce, **"Ya Ubangiji, kai ne haskena, kana haskaka duhuna"** (2 Sama'ila 22:29).

Sa'ad da muka san Yesu, muka san Allah. Yesu ya ce, **"Da kun san ni, da kun san Ubana ma"** (Yahaya 14:7a). **"Domin shi Allah wanda ya ce, 'Haske yă ɓullo daga duhu ya haskaka,' shi ne ya haskaka zukatanmu domin a haskaka**

**mutane su san ɗaukakarsa a fuskar Yesu Almasihu"** (2 Korantiyawa 4:6). Kai, ka karɓi hasken nan?

## Tafiya Cikin Hasken

Su waɗanda suke bin Yesu ba su yi tafiya cikin duhu ba amma cikin haske. **"Domin dā ku duhu ne, amma yanzu ku haske ne cikin Ubangiji. Ku yi zaman mutanen haske"** (Afisawa 5:8). **"Hanyar mugaye kuwa duhu ne baƙi ƙirin, kamar duhun dare. Sukan fāɗi, amma ba su san abin da ya sa suka yi tuntuɓe ba"** (Karin Magana 4:19). **"Hanyar da adalai ke bi kamar fitowar rana ce, sai ta yi ta ƙara haske, har ta take tsaka"** (Karin Magana 4:18).

Maganar Allah haske ne. **"Maganarka fitila ce wadda za ta bi da ni, haske ne kuma a kan hanyata"** (Zabura 119:105). **"Fassarar koyarwarka takan ba da haske, takan ba da hikima ga wanda bai ƙware ba"** (Zabura 119:130). Idan mun karanta maganar Allah kowace rana, wajib ne mu ji ta, mu yi biyayya ga abin da ta ce. Wannan shi ne abin da ake nufi da cewa, "Ku yi tafiya cikin haske." Aikata abin da Allah ya ce, shi ne tafiya cikin haske. Ka tuna umarni da Yesu ya yi cewa, "Ku ƙaunaci juna." Shi ne dalilin da Maganar Allah ta ce, **"Mai ƙin ɗan'uwansa kuwa, a duhu yake, a cikin duhu yake tafiya, bai san ma inda yake sa ƙafa ba, domin duhun ya makantar da shi"** (1 Yahaya 2:11).

Hanyar yin makamta shi ne a yi tafiya cikin duhu kullayaumi. Wajib ne mu yi ta yi tafiya cikin haske, ko idanun zuciyarmu za su makanta sabili da Shaiɗan zai ruɗe mu, mu koma cikin duhu.

## Mu Ne Haske Cikin Duniya

**"Kome za ka yi kada ku yi shi da gunaguni ko gardama, don ku zama marasa abin zargi, sahihai, 'ya'yan Allah marasa aibu a zamanin mutane karkatattu, kangararru, waɗanda kuke haskakawa a cikinsu kamar fitilu a duniya"** (Filibiyawa 2:14, 15). Allah ya zaɓe mu **"domin ku sanar da mafifitan al'amuran wannan da ya kirawo ku daga cikin duhu, kuka shiga**

**maɗaukakin haskensa"** (1 Bitrus 2:9b). Rayuwarka haske ne ga su waɗanda ke kewaye da kai? In ba haka ba, Manzon Bulus ya ce, **"Sai mu watsar da ayyukan duhu, mu yi ɗamara da kayan ɗamara na haske"** (Romawa 13:12b).

Muke da bukata mu zama da shiri domin zuwan Yesu a duniya. Sai dai idan mun falka, muna tafiya cikin haske, za mu zama da shiri don zuwansa. **"Domin duk mutanen haske kuke, na rana kuma. Mu ba na dare ko na duhu ba ne. Ashe, saboda haka kada mu yi barci yadda waɗansu ke yi, sai dai mu zauna a faɗake, da natsuwa"** (1 Tasalonikawa 5:5, 6).

Yesu ya ce, sa'ad da ya ba da labarin sabon sama, da sabon duniya, da sabon Urushalima **"ba ya bukatar rana ko wata su haskaka shi, domin ɗaukakar Allah ita ce haskensa, Ɗan Ragon kuma fitilarsa"** (Wahayin Yahaya 21:23b). Ba abin murna ne Yesu zai zama haskenmu har abada abadin ba!

## Yi Aiki Tun Akwai Haske

Muna bukata mu yi aiki har ran da Yesu ya dawo domin mu haskaka cikin wannan duniya mai duhu. Wata rana wannan duniya za ta shuɗe (Matiyu 5:18). Su waɗanda ba su zo wurin haske ba za a jefa su cikin matsanancin duhu (Matiyu 22:13). Bari mu yi aiki **"Domin ka buɗe musu ido, su juyo daga duhu zuwa haske, daga kuma mulkin Shaiɗan zuwa wurin Allah, domin su sami gafarar zunubai"** (Ayyukan Manzanni 26:18a).

Wata rana Yahudawa suka tambayi Yesu, **"Me za mu yi mu aikata ayyukan da Allah ke so?"** Yesu ya amsa musu ya ce, **"Wannan shi ne aikin da Allah ke so, wato ku gaskata da wanda ya aiko"** (Yahaya 6:28b, 29b). Yesu ya koya musu cewa, **"Domin in ba ku gaskata ni ne shi ba, za ku mutu da zunubanku"** (Yahaya 8:24b).

Da fari, dole ne mu da kanmu mu tabbata mun zo gun hasken domin mu karɓi rai madawwami. Sa'an nan sai mu yi aiki tare da Yesu domin mu kawo waɗansu ga Hasken. Yesu ya ce, **"Kada ku yi wahala a kan neman abinci mai lalacewa, sai dai a kan abinci mai dawwama har ya zuwa rai madawwami, wanda Ɗan Mutum zai ba ku"** (Yahaya 6:27a).

Ka tuna da makafon daga cikin labarin da ka karanta? Ya gaya ma waɗansu abin da Yesu ya yi masa gabagaɗi. Ko da shi ke su waɗanda ke cikin duhu a ruhaniya suka ƙore shi daga Haika-

li, Yesu ya kula da shi, ya zo wurinsa don ya ƙara bayyana masa kansa. Zai yi maka hakanan kuma!

## LABARI NA 15. YESU SHI NE MAKIYAYI MAI KYAU



Yahaya 10:1-16, 27-33

1"Lalle hakika, ina gaya muku,
wanda bai shiga garken tumaki
ta ƙofa ba, amma ya haura ta
wani gu, to, shi ɓarawo ne, ɗan
fashi kuma. 2Wanda kuwa ya
shiga ta ƙofar, makiyayin tuma-
kin ne. 3Mai tsaron ƙofar yakan
buɗe masa, tumakin kuma su-
kan saurari murya tasa, yakan
kama sunan nasa tumaki, ya
kai su waje. 4Bayan ya fitar da
dukan nasa waje, sai ya shige
gabansu, tumakin na biye na
shi, domin sun san murya tasa.
5Ba za su bi baƙo ba, sai dai su
guje shi, don ba su san mur-
yar baƙo ba."6Yesu ya yi musu
wannan misali, amma ba su ga-
ne abin da ya faɗa musu ba.
7Don haka Yesu ya sāke ce
musu, "Lalle hakika, ina gaya
muku, ni ne ƙofar tumakin.
8Duk waɗanda suka riga ni zu-
wa cewa su ne ni, ɓarayi ne,
'yan fashi kuma, amma tuma-
kin ba su kula da su ba. 9Ni ne
ƙofar. Kowa ya shiga ta wurina
zai sami ceto, ya kai ya kawo,
ya kuma yi kiwo. 10Ɓarawo ya-
kan zo ne kawai don sata da
kisa da hallakarwa. Ni kuwa
na zo ne domin su sami rai, su
kuma same shi a yalwace. 11Ni
ne Makiyayi mai kyau. Maki-
yayi mai kyau kuwa shi ne mai
ba da ransa maimakon tuma-
kin. 12Wanda ke ɗan asako ku-
wa, ba makiyayin gaske ba, tu-
makin kuma ba nasa ba, da
ganin kyarkeci ya doso, sai ya
watsar da tumakin, ya yi ta
kansa, kyarkeci kuwa ya sure
waɗansu, ya fasa sauran. 13Ya
gudu ne fa, don shi ɗan asako
ne, ba abin da ya dame shi da
tumakin. 14Ni ne Makiyayi mai
kyau. Na san nawa, nawa ku-
ma sun san ni, 15kamar yadda
Uba ya san ni, ni kuma na san
Uban. Ina ba da raina maima-
kon tumakin. 16Ina kuma da

waɗansu tumaki da ba na wannan garke ba ne. Su ma lalle in kawo su, za su kuwa saurari muryata, su zama garke guda, makiyayi kuma guda.
[27]Tumakin nan nawa sukan saurari muryata, na san su, suna kuma bina. [28]Ina ba su rai madawwami, ba kuwa za su halaka ba har abada, ba kuma mai ƙwace su daga hannuna. [29]Ubana, wanda ya ba ni su, ya fi duka girma, ba kuwa mai iya ƙwace su daga ikon Uban. [30]Ni da Uba ɗaya muke." [31]Sai Yahudawa suka sāke ɗebo duwatsu su jajjefe shi. [32]Yesu ya amsa musu ya ce, "Na nuna muku ayyuka nagari masu yawa daga wurin Uba, a kan wanne a cikinsu za ku jajjefe ni?" [33]Yahudawa suka amsa masa suka ce, "Ba don wani aiki nagari za mu jajjefe ka ba, sai don saɓo, don kai, ga ka mutum, amma kana mai da kanka Allah."

## Abin Koyarwa Daga Cikin Wannan Labari

1. Yesu, shi kaɗai ne, ƙofa zuwa ga sabon rai. Ta wurin jin muryarsa, da kuma binsa kaɗai, za mu iya zama tumakinsa. Yakan kira ka da sunanka. Yakan bishe ka, yakan ciyadda kai, ya ba da ransa dominka. **"Dukanmu muna kama da tumakin da suka ɓata, kowannenmu ya kama hanyarsa. Sai Ubangiji ya sa hukunci ya auko a kansa, hukuncin da ya wajaba a kanmu"** (Ishaya 53:6). Ai kuwa, ka juyo da bin hanyarka ka bi nasa hanya?

2. Yesu kaɗai, shi ne makiyayi mai gaskiya. **"Shi ne Allahnmu, mu ne jama'ar da yake lura da ita, mu ne kuma garken da yake ciyarwa"** (Zabura 95:7a). **"Kada fa a manta da cewa, Ubangiji shi ne Allah! Shi ne ya yi mu, mu kuwa nasa ne, mu jama'arsa ne, mu garkensa ne"** (Zabura 100:3).

3. Idan mu ne tumakinsa, ya san mu, mu kuma mun san shi. **"Amma kai, ya Ubangiji, kana sane da ni, kana ganina, kai kanka kake gwada tunanina"** (Irmiya 12:3a). Ka sani Yesu shi makiyayenka ne? In haka ne, za ka bi shi, shi kaɗai, ba za ka bi wani ba. Makiyayin ya san ka? Sa'ad da makiyayin Mai Girma ya dawo, su dayawa za su ce masa, **"'Ya Ubangiji, ya Ubangiji, ashe, ba mu yi annabci da sunanka ba? Ba mu fitar da aljannu da sunanka ba? Ba mu kuma yi ayyukan al'ajabi masu yawa da sunanka ba?'"** Yesu ya ce, **"Sa'an nan zan ce musu, 'Ni ban taɓa saninku ba. Ku rabu da ni, ku masu yin mugun aiki'"** (Matiyu 7:22, 23). Ba shi yiwuwa mu zama tumakin Yesu, mu bi

hanyar kanmu gaba ɗaya ba. "Ku kuma zama a tsarkake, in banda shi kuwa, ba wanda zai ga Ubangiji" (Ibraniyawa 12:14).

4. Sa'ad da mun zama na Yesu almasihu, mu nasa ne har abada. Ba wanda ya iya ƙwace mu daga hannunsa. Wannan alkawari domin su waɗanda suke bin Makiyayi Mai Kyau, Ubangiji Yesu Almasihu.

5. Wanda ke bin Yesu za shi guje ma baƙo. Shaiɗan kamar ɓarawo ne, ɗan fashi wanda yake so ya yi sata, ya kashe, ya halaka.

6. Yesu ya ce shi Allah ne. Sa'ad da Yesu ya ce shi da Uba guda ne, ya ce shi Allah ne. Su Yahudawa sun sani shi yana mai da kansa daidai da Allah. Da suna bin Allah, da sun sani Yesu shi ne Makiyayinsu ne, yadda Ishaya ya yi anabaci cewa, **"Ubangiji yana zuwa ya yi mulki da iko . . . Zai lura da garkensa kama yadda makiyayi ke yi, zai tattara 'yan raguna wuri ɗaya, zai ɗauƙe su ya rungume su, a hankali zai bi da iyayensu"** (Ishaya 40:10, 11).

## Zaburar Makiyayi

**Zabura 23**

**1 Ubangiji makiyayina ne, ba zan rasa kome ba. 2 Yana sa ni in huta a saura mai ɗanyar ciyawa, yana bi da ni a tafkuna masu daɗin ruwa, suna kwance lif. 3 Yana ba ni sabon ƙarfi. Yana bi da ni a hanyar da ke daidai kamar yadda ya alkawarta. 4 Ko da hanyan nan ta bi ta tsakiyar duhu na mutuwa, ba zan ji tsoro ba, ya Ubangiji, gama kana tare da ni! Sandanka na makiyayi da kerenka suna kiyaye lafiyata. 5 Ka shirya mini liyafa inda maƙiyana duk za su iya ganina, ka marabce ni, ka shafe kaina da mai, ka cika tanduna fal da mai. 6 Hakika, alherinka da ƙaunarka, za su kasance tare da ni muddin raina. Haikalinka zai zama gidana har abada.**



# LABARI NA 16. YESU SHI NE TASHIN MATATTU DA RAI

Yahaya 11:1-7, 17-46

1Wani mutum ne ya yi rashin lafiya, sunansa Li'azaru na Betanya, ƙauyen su Maryamu da 'yar'uwarta Marta. 2Maryamun nan kuwa, wadda ɗan'uwanta Li'azaru ba shi da lafiya, ita ce wadda ta shafa wa Ubangiji man ƙanshi, ta kuma shafe ƙafafunsa da gashinta. 3To, 'yan'uwan nan mata suka aika masa, suka ce, "Ya Ubangiji, ga shi, wanda kake ƙaunan nan ba shi da lafiya." 4Da Yesu ya ji haka ya ce, "Wannan rashin lafiya, ƙarshensa ba mutuwa ba ne, domin a ɗaukaka Allah ne, a kuma ɗaukaka Ɗan Allah ta wurinsa."

5Yesu kuwa na ƙaunar Marta da 'yar'uwa tata, da kuma Li'azaru. 6To, da ya ji Li'azaru ba shi da lafiya, ya ƙara kwana biyu a wurin da yake. 7Bayan haka ya ce wa almajirai, "Mu koma ƙasar Yahudiya."

17Da Yesu ya isa, ya tarar Li'azaru, har ya kwana huɗu a kabari. 18Betanya kuwa kusa da Urushalima take, misalin mil biyu. 19Yahudawa da yawa sun zo yi wa Marta da Maryamu ta'aziyyar ɗan'uwansu. 20Da jin Yesu na zuwa, sai Marta ta je taryensa, Maryamu kuwa ta zauna a gida. 21Sai Marta ta ce wa Yesu, "Ya Ubangiji, da kana nan da ɗan'uwana bai mutu ba. 22Koyanzu ma na sani kome ka roƙi Allah, zai yi maka." 23Yesu ya ce mata, "Ɗan'uwanki zai tashi." 24Marta ta ce masa, "Na sani zai tashi a tashin matattu a ranar ƙarshe." 25Yesu ya ce mata, "Ai, ni ne tashin matattu, ni ne kuma rai. Wanda ya gaskata da ni, ko ya mutu zai rayu. 26Wanda kuwa ke raye, yake kuma gaskatawa da ni, ba zai mutu ba har abada. Kin gaskata wannan?" 27Ta ce masa, "I, ya Ubangiji. Na gaskata kai ne Almasihu, Ɗan Allah, shi wannan mai zuwa duniya."

28Da ta faɗi haka, ta je ta kirawo 'yar'uwa tata Maryamu, ta raɗa mata ta ce, "Ga Malam ya zo, yana kiranki." 29Ita kuwa da jin haka, ta yi maza ta tashi ta nufi wurinsa. 30Yesu

dai bai iso ƙauyen ba tukuna, har yanzu yana wurin da Marta ta tarye shi. [31]Da Yahudawan da ke tare da ita cikin gida suna mata ta'aziyya suka ga Maryamu ta yi maza ta tashi ta fita, suka bi ta, suna zaton za ta kabarin ne, ta yi kuka a can. [32]Da Maryamu ta iso inda Yesu yake, ta gan shi, sai ta faɗi a gabansa ta ce masa, "Ya Ubangiji, da kana nan da dan'uwana bai mutu ba."

[33]Da Yesu ya ga tana kuka, Yahudawan da suka zo tare da ita su ma, suna kuka, sai ya nisa a ransa, ya yi juyayi gaya. [34]Ya kuma ce, "Ina kuka sa shi?" Suka ce masa, "Ya Ubangiji, zo ka gani."

[35]Sai Yesu ya yi hawaye. [36]Don haka Yahudawa suka ce, "Dubi yadda yake ƙaunarsa!" [37]Amma waɗansunsu suka ce, "Ashe, wanda ya buɗe wa makahon nan ido, ba zai iya hana wannan mutum mutuwa ba?"

[38]Sai Yesu ya sāke nisawa a ransa, ya iso kabarin. Kabarin kuwa kogon dutse ne, da wani dutse kuma an rufe bakin. [39]Yesu ya ce, "Ku kawar da dutsen." Sai Marta, 'yar'uwar mamacin, ta ce masa, "Ya Ubangiji, ai, yanzu ya yi ɗoyi, don yau kwanansa huɗu ke nan da mutuwa." [40]Sai Yesu ya ce mata, "Ban gaya miki ba, in kin ba da gaskiya za ki ga ɗaukakar Allah?" [41]Sai suka kawar da dutsen. Yesu kuwa ya ɗaga kai sama ya ce, "Ya Uba, na gode maka da ka saurare ni. [42]Ko dā ma na sani koyaushe kana saurarona, amma na faɗi haka ne saboda jama'ar da ke nan tsaitsaye, domin su gaskata kai ne ka aiko ni." [43]Da ya faɗi haka ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, Li'azaru, fito!" [44]Sai mamacin ya fito, ƙafa da hannu a ɗaure da abin likkafani, fuska tasa kuma a naɗe da mayani. Yesu ya ce musu, "Ku kwance masa, ya tafi." [45]Saboda haka Yahudawa



da yawa da suka zo wurin Maryamu, suka kuma ga abin da ya yi, suka gaskata da shi.

46Amma waɗansunsu suka tafi wurin Farisiyawa, suka gaya musu abin da Yesu ya yi.

## Abin Tunani

Ba abin farin ciki ne Yesu ya ƙaunaci abokansa da ƙauna mai yawa haka? Kai, abokinsa ne kuma, idan kake yin abin da ya faɗi (Yahaya 15:14). Cikin labarin nan abokan Yesu suna da baƙin ciki. Ɗan'uwansu Li'azaru ya rasu. Da fari, suka gani kamar Yesu bai kula ba. Kai, ma, ka taɓa yi tunani cewa, Yesu bai kula ba, sa'ad da kake da baƙin ciki? Allah bai kan yi kwana ba. Kowane lokaci ya san abin da yake yi. Wajib ne mu riƙa dogara gareshi, shi zai yi abin da zai fi kawo masa daraja.

Allah yake da dabara dominka kuma. Yana son ya maishe ka kamar Ɗansa Yesu. **"Mun kuma sani al'amura duka na aikatawa tare zuwa alheri ga waɗanda ke ƙaunar Allah, wato waɗanda ke kirayayyu bisa ga nufinsa. Waɗanda Allah ya riga ya zaɓa tuntuni, su ne ya ƙaddara su ɗauki kamannin Ɗansa, domin shi Ɗan yǎ zama na farko cikin 'yan'uwa masu yawa"** (Romawa 8:28, 29). Shi ne dalilin da mu kan sha wuya wani lokaci. **"Wannan kuwa domin a tabbatar da sahihancin bangaskiyarku ne (wadda ta fi zinariya daraja nesa, ita zinariya kuwa–ko da ya ke mai ƙarewa ce–akan jarraba ta da wuta), domin bangaskiyan nan taku tǎ jawo muku yabo da girma da ɗaukaka a bayyanar Yesu Almasihu"** (1 Bitrus 1:7).

Yesu yake so ya koya wa Marta da Maryamu, da mu kuma, idan muke gaskata shi ba za mu taɓa mutuwa ba. Sa'ad da su waɗanda suke gaskata shi sun mutu sun **"rabu da jikin nan"** amma sun **"zauna a gun Ubangiji"** (2 Korantiyawa 5:8). Yesu ya tabbata musu yake da iko ya ta da matattu da ya kira sunan Li'azaru. [Li'azaru ya ji Yesu ya kira sunansa, ya tashi, ya rayu.] Lokacin da Yesu zai dawo duniyanga, **"matattu za su ji muryar Ɗan Allah, masu ji kuwa su rayu"** (Yahaya 5:25b).

Ko yanzu, Yesu yana ƙwanƙwasa a ƙofar zukatan. **"Kowa ya**

**ji muryata ya buɗe ƙofar, sai in shiga wurinsa"** (Wahayin Yahaya 3:20). Su waɗanda suka ji muryarsa su buɗe ƙofar zuciyarsu za su zama sabon halitta. **"Ku kuma yā raya ku sa'ad da kuke matattu ta laifofinku da zunubanku"** (Afisawa 2:1). **"Haka ku ma sai ku lasafta kanku kamar ku matattu ne ga zunubi, amma kuna raye, rayuwa ga Allah, ta Almasihu Yesu. Saboda haka kada ku yarda zunubi ya mallaki jikin nan naku mai mutuwa, har da za ku biye wa muguwar sha'awa tasa. Kada kuma ku miƙa gaɓoɓinku su zama kayan aikin mugunta don yin zunubi. Amma ku miƙa kanku ga Allah kamar waɗanda aka raya bayan mutuwa, kuna miƙa gaɓoɓinku ga Allah kayan aikin adalci"** (Romawa 6:11-13).

## In Kana So A Yi Aikin Al'ajabi, Dole Ne Ka Yi Biyayya

Kana da wata damuwa ko wahala da kake bukata Allah ya yi maka aikin al'ajibi? Kila Yesu zai yarda waɗansu abubuwa masu wuya su same ka "domin a ɗaukaka Allah a cikinka." Kada ka manta, yana ƙaunace ka yadda ya ƙaunaci Marta da Maryamu. Kila yana shirin wata mu'ujiza wadda ba ka yi tsammani ba. Ka lura, dole ne su yi biyayya kafin wannan mu'ujiza na sabon rai ya faru. Yesu ya ce, "Ku kawar da dutsen." Ko da shi ke ba su yi tsammani wannan zai yi kyau ba, suka yi shi. Suka yi masa biyayya. Bayan da Li'azaru ya fito kabarin, Yesu ya ce, "Ku kwance masa, ya tafi."

Domin a ga darajar ikon Allah, dole mu kuma mu yi biyayya cikin dukan abubuwa kome ƙaramancinsu, wanda Ruhu Mai Tsarki ya nuna mana. Idan muna bukata mu roƙi wani shi gafarta mana, ko ba mu yi masa laifi sosai ba, dole mu yi shi. Kila shi ne dutsen da dole a kawar kafin Yesu ya iya yin aikin al'ajabi a zuciyar wani. Sa'ad da Yesu ya yi aikin al'ajibi, bari dai mu taimaki waɗansu a kawar masu abubuwan da ke hana su, su sami yanci cikin Yesu. Ba abin godiya ne Yesu ya yarda abokansa suka yi taimako cikin wannan aikin al'ajibi?

# LABARI NA 17. MANYAN FIRISTOCI DA FARISIYAWA SUKA NEMA SU KASHE YESU

**Yahaya 11:47-53**

**47Don haka manyan firistoci
da Farisiyawa suka tara 'yan
majalisa, suka ce, "Shin, me
muke yi ne, har mutumin nan
yake ta yin mu'ujizai da yawa
haka? 48In fa muka ƙyale shi
kan haka, kowa zai gaskata da
shi, Romawa kuma za su zo su
karɓe ƙasarmu su ɗebe jama'ar-
mu." 49Amma ɗayansu, wai shi
Kayafa, wanda yake shi ne
babban firist a shekaran nan,
ya ce musu, "Ku dai ba ku
san kome ba. 50Ba kwa lura,
ai, ya fiye muku mutum ɗaya
ya mutu saboda jama'a, da duk
jama'a ta halaka." 51Ba da nu-
finsa ya faɗi haka ba, sai dai
da ya ke shi ne babban firist a
shekaran nan, ya yi annabci
cewa Yesu zai mutu saboda ja-
ma'a, 52ba ma saboda jama'a
kaɗai ba, har ma yǎ tattaro
'ya'yan Allah da ke warwatse
ko'ina su zama ɗaya. 53Daga
ran nan fa sai suka ƙulla su ka-
she shi.**

## Suka Ki Sarkinsu

Manyan Firistoci da Farisiyawa suka ga mu'ujizai waɗanda Yesu ya yi. Suka ji koyarwa da ya yi cewa, shi da Ubansa ɗaya ne, da kuma "tun ba a haifi Ibrahim ba ni ne" (Yahaya 8:58). Amma duk da haka ba su iya su gaskata Yesu shi ne Almasihu nasu, wanda an alkawarta masu ke zuwa ba.

Labari ɗin ya nuna su ba su yarda su bar matsayinsu ba, wato sun zama kamar mugun barori cikin labari da Yesu ya ba su cewa, **"Ba sa so ya yi mulki a kansu"** (Luke 19:14b). Sai shugabannin Yahudawa suka ƙulle shawara za su kashe mutum ɗaya-Yesu-don kada mulki duka ya sha wuya. Amma, lalle, ba su iya yi masa kome ba idan Yesu bai yarda ya ba da ransa ba.

Nufin Allah ne Yesu ya ba da ransa tun kafin an yi duniya, domin a ceci dukan duniya. **"Ubangiji ya ce, Nufina ne ya sha wahala, mutuwar kuwa hadaya ce domin ta kawo gafara, saboda haka zai ga zuriyarsa, zai yi tsawon rai, ta wurinsa nufina zai cika"** (Ishaya 53:10).

# LABARI NA 18. LABARIN KYAUTA MAI TAMANI DA YAWA



Yahaya 12:1-8

[1]Idin Ketarewa saura kwana
shida, sai Yesu ya zo Betanya
inda Li'azaru yake, wanda Ye-
su ya tasa daga matattu. [2]Nan
aka yi masa abincin dare, Mar-
ta ce ta yi hidima, Li'azaru
kuwa yana cikin masu ci tare
da shi. [3]Sai Maryamu ta ɗauko
awo guda na man ƙanshi na
nardi tsantsa, mai tamanin gas-
ke, ta shafa a ƙafafun Yesu,
sa'an nan ta shafe su da ga-
shinta. Duk gidan ya game da
ƙanshin man. [4]Amma Yahuza
Iskariyoti, ɗaya daga cikin al-
majiransa, wato wanda zai ba-
she shi, ya ce, [5]"Me ya hana a
sayar da man nan a kan dinari
ɗari uku, a ba gajiyayyu kuɗ-
in?" [6]Ya faɗi haka fa, ba wai
don yana kula da gajiyayyu
ba, a'a, sai dai don shi ɓarawo
ne, da ya ke kuma jakar ku-
ɗinsu na hannunsa yakan riƙa
taɓa abin da ke ciki. [7]Sai Yesu
ya ce, "A ƙyale ta, ta ajiye shi
domin tanadin ranar jana'iza-
ta." [8]Ai, kullum kuna tare da
gajiyayyu, amma ba kullum ku-
ke tare da ni ba."

## Yesu Ya Isa Ɗaukakawa Mai Girma

Lokacin da Yesu ya ta da Li'azaru daga matattu Shugabannin Yahudawa suka yarda cewa, dole Yesu ya mutu. Amma abokannin Yesu suka yi murna, suka cika da godiya har suka yi wani biki domin a girmama Yesu. Yanzu Maryamu ta san Yesu wanene ne. Kamnarta dominsa ta sa ta ba da man ƙanshi, mai tamanin gaske–kila wajen kuɗin aiki na kwana 300. Maryamu ta gane maganar Yesu cewa za a gicciye shi ba da daɗewa ba (Matiyu 26:2).

**"Macancanci ne kai, ya Ubangiji Allahnmu, kă sami ɗaukaka, da girma, da iko, domin kai ne ka halicci dukkan abubuwa, da nufinka ne suka kasance aka kuma halicce su"** (Wahayin Yahaya 4:11).

Yahaya ya nuna daɗin sama sa'ad da ya rubuta abin da ya gani can lokacin da jama'ar mutanen Allah suke kewaye da kursiyinsa. Mala'iku, yawansu zambar dubu har duban dubbai suna yabe shi cewa, **"Macancanci ne Ɗan Ragon nan da aka yanka yă sami iko, da wadata, da hikima, da ƙarfi, da girma, da ɗaukaka, da yabo!"** (Wahayin Yahaya 5:12b). Yesu almasihu shi ne macancanci na dukan yabo da sujada da mun iya yi masa.

## Kyautai Da Muka Iya Ba Yesu

Me muka iya ba Yesu don mu nuna masa godiyarmu? Bulus ya ce, **"Don haka ina roƙonku 'yan'uwa, saboda yawan jinƙai na Allah, ku miƙa jikinku hadaya rayayyiya, tsattsarka, abar karɓa ga Allah. Domin wannan ita ce ibadarku ta ainihi. Kada ku biye wa zamanin nan, amma ku bar halinku ya sake ta wurin sabunta hankalinku ɗungum, don ku tabbatar da abin da Allah ke so, wato nufinsa kyakkyawa, abin karɓa, cikakke kuma"** (Romawa 12:1, 2). Bari mu ba da jikunanmu ga Yesu, ta wurin yin rayuwarmu don mu gamshe shi. Bari mu ba da tunaninmu da azancinmu don mu yi tunani akan sunansa, da Maganarsa, da aikinsa maimakon mu yi tunanin abubuwan duniya kurum.

Waɗansu mutane za su yi tsammani muna ɓatar da rayuwarmu da iyawarmu banza in muna bauta ma Ubangiji. Yahuza ya yi tsammani Maryamu ta ɓatar da man nan nata banza? Ina Yahuza yau? **"Tunawa da mutumin kirki albarka ce, amma nan da nan za a manta da mugaye"** (Karin Magana 10:7). **"Mutumin kirki ba zai kāsa ba daɗai, ba za a taɓa mantuwa da shi ba"** (Zabura 112:6).

Sa'ad da muka nuna ƙamna ga 'yanuwanmu cikin Almasihu, muna ɗaukaka Almasihu Yesu wanda ke zamne cikinsu. Kana yi wa iyayenka masu bi, ko matarki, ko mijinki, ko 'ya'yanka, kamar yadda kana yi wa Yesu? Mukan ɗaukaka Yesu kuma sa'ad da muke ƙaunaci abokan gabanmu, domin Yesu ya ce mu yi haka (Matiyu 5:44).

Yesu ya ƙaunace mu da yawa har ya ba da kansa dominmu, **"Ya kuma ba da kansa dominmu, sadaka mai ƙanshi, hadaya kuma ga Allah"** (Afisawa 5:2b). **"To, koyaushe sai mu yi ta yabon Allah ta wurinsa, sadakar da muke miƙawa ke nan, wato mu yabe shi, muna ta ɗaukaka sunansa"** (Ibraniyawa 13:15).

# LABARI NA 19. LABARIN SARKI MAI TAWALI'U



Yahaya 12:12-16
[12]Kashegari babban taron da suka zo idi, da suka ji Yesu na zuwa Urushalima, [13]suka ɗaɗɗauko gazarin dabino suka firfita taryensa, suna ta da murya suna cewa, "Hosanna! Albarka ta tabbata ga mai zuwa da sunan Ubangiji, Sarkin Isra'ila!" [14]Da Yesu ya sami wani ɗan jaki sai ya hau, yadda yake a rubuce cewa, [15]"Kada ki ji tsoro, ya ke 'yar Sihiyona, Ga Sarkinki na zuwa a kan aholakin jaki!" [16]Da fari almajiransa ba su gane abin nan ba, amma bayan an ɗaukaka Yesu, suka tuna abin nan a rubuce yake game da shi, har ma aka yi masa shi.

## Yesu Zai Dawo Sarki Mai Ɗaukaka

Wani annabi a Tsohon Alkawari ya ce, **"Ki yi murna ƙwarai, ya Sihiyona! Ta da murya ya Urushalima! Ga Sarkinki yana zuwa wurinki, shi mai adalci ne, mai nasara, shi kuma mai tawali'u ne, yana bisa kan jaki, a kan aholaki"** (Zakariya 9:9). I, annabawa suka ba da labarin zuwan Yesu kamar mutum, kamar mai ceto, kamar bawa. Annabci fiye da 300 suka cika lokacin da Yesu ya zo ya yi zamansa a duniya, da mutuwarsa da tashinsa kuma. Amma annabci fiye da haka sau uku za su cika sa'ad da Yesu ya sake zuwa a duniya Sarkin Daraja domin ya yi mulkin duniya shekara dubu (Wahayin Yahaya 20:4).


**"Domin Ubangiji kansa ma zai sauko daga Sama da kira mai ƙarfi, da muryar babban mala'ika, da kuma busar ƙahon Allah. Waɗanda suka mutu suna na Almasihu, su ne za su fara tashi, sa'an nan sai mu da muka wanzu, muke raye, za a ɗauke mu tare da su ta cikin gajimare, mu sadu da Ubangiji a sararin sama, sai kuma kullum mu kasance tare da Ubangiji"** (1 Tasalonikawa 4:16, 17).

**"A ranar bayyanar Ubangiji Yesu daga Sama tare da manyan mala'ikunsa, a cikin wuta mai ruruwa, yana ta saka wa waɗanda suka ƙi sanin Allah, da kuma waɗanda suka ƙi bin bisharar Ubangijinmu Yesu"** (2 Tasalonikawa 1:7b, 8).

## Ka Yi Shiri Don Zuwansa?

Allah yakan cika alkawarinsa. Bai zo da sauri ba domin yana so mutane da yawa su tuba tukuna. **"Ubangiji ba ya jinkirta alkawarinsa,...ba ya so kowa ya halaka, sai dai kowa ya kai ga tuba"** (2 Bitrus 3:9). Yana zuwa, kila ba da daɗewa ba! Kana da shiri, kana yin zaman tsarki, kana jawo waɗansu gareshi? **"Duk da haka ranar Ubangiji za ta zo kamar ɓarawo, sa'an nan sammai za su shuɗe da ƙara mai tsanani, dukkan abin da ke cikinsu za su ƙone, su halaka, ƙasa kuma da abubuwan da ke kanta duk za su ɓăce. Tun da ya ke duk abubuwan nan za a hallaka su haka, waɗanne irin mutane ya kamata ku zama? Ya kamata ku yi zaman tsarkaka masu ibada"** (2 Bitrus 3:10, 11).

# LABARI NA 20. LABARIN KWAYAR ALKAMA



Yahaya 12:24-26

[24]Lalle hakika, ina gaya muku, in ba an binne ƙwayar alkama ta mutu ba, za ta zauna ita kaɗai. Amma in ta mutu sai ta hayayyafa. [25]Mai ƙaunar ransa zai rasa shi. Wanda kuwa ya ƙi ransa a duniyan nan, ya kiyaye shi ke nan, har ya zuwa rai madawwami. [26]Wanda duk zai bauta mini, ya bi ni. Inda nake kuma, nan bawana zai kasance shi ma. Kowa ke bauta mini, Uba za girmama shi."

## Yaya Mutuwa Ta Ke

Mutuwa ta kan zo kafin ikon tashin matattu. Haka yake wurin Yesu, haka zai zama garemu. Manzon Bulus ya nuna mana ma'anar mutuwa, sai mu mutu ga kanmu sabili da Yesu. **"Amma dai kowace irin riba na taɓa ci, na ɗauka hasara ce sa-**

**boda Almasihu. Muradina ke nan in san Almasihu, in san ikon tashinsa daga matattu"** (Filibiyawa 3:7, 10a).

Sau dayawa in mun yi biyayya ga Almasihu dole ne nufin kanmu ya mutu, amma sa'ad da mun mutu ga kanmu, ikon Almasihu zai aikata nufinsa a cikinmu. Mu kan lissafta kanmu mataci tare da Almasihu; sabon rai da ke cikinmu zai rayu ta wurin bangaskiya sa'ad da mun yi masa biyayya. **"An gicciye ni tare da Almasihu. Yanzu ba ni ne kuma ke raye ba, Almasihu ne ke raye a cikina. Rayuwan nan kuma da nake yi ta jiki, rayuwa ce ta wurin bangaskiya ga Ɗan Allah, wanda ya ƙaunace ni, har ya ba da kansa domina"** (Galatiyawa 2:20). **"In kuna zaman halin mutuntaka, za ku mutu ke nan, amma in da ikon Ruhu kuka kashe ayyukan nan na halin mutuntaka, sai ku rayu"** (Romawa 8:13). Bari Ruhun Allah ya nuna maka abubuwan da ya kamata ka mai da su mattace cikin rayuwarka: ko kila wani mugun hali ne, ko wani mugun ra'ayi ne. Lokacin da ka mai da su matacce, ka yi biyayya, za ka gani ikon Allah zai ƙarfafa ka cikin sabon rai. Zai ba ka iko ka yi sabon hali da sabon ra'ayi, don ka ci nasara a rayuwarka. **"Domin Allah shi ne mai aiki a zukatanku ku nufi abin da ke kyakkyawan nufinsa, ku kuma aikata shi"** (Filibiyawa 2:13).

## LABARI NA 21. YESU YA YI KOYARWA TA WURIN MISALI DA UMURNI

**Yahaya 13:3-17, 34, 35**



**3Yesu kuwa, da ya ke ya san Uba ya sa kome a hannunsa, ya kuma sani daga wurin Allah ya fito, wurin Allah kuma zai koma, 4sai ya tashi daga cin abincin, ya ajiye mayafinsa, ya ɗauko ɗan zane ya yi ɗamara da shi. 5Sa'an nan ya zuba ruwa a daro, ya fara wanke ƙafafun almajiran, yana shafe su da abin da ya yi ɗamara da**

shi. [6]Sai ya zo ga Bitrus, shi kuwa ya ce masa, "Ya Ubangiji, ashe, kai ne za ka wanke mini ƙafa?" [7]Yesu ya amsa masa ya ce, "Yanzu kam, ba ka san abin da nake yi ba, amma daga baya za ka fahimta." [8]Bitrus ya ce masa, "Wane ni! Ai, ba za ka wanke mini ƙafa ba har abada!" Yesu ya amsa masa ya ce, "In ban wanke maka ba, ba ka da rabo a gare ni." [9]Bitrus ya ce masa, "Ya Ubangiji, ba ma ƙafafuna kaɗai ba, har ma da hannuwana da kaina!" [10]Yesu ya ce masa, "Wanda ya yi wanka ba ya bukatar wanke kome, sai ƙafafunsa kawai, domin ya riga ya tsarkaka sarai. Ku ma tsarkakakku ne, amma ba dukanku ba." [11]Don ya san wanda zai bashe shi, shi ya sa ya ce, "Ba dukanku ne tsarkakakku ba." [12]Bayan ya wanke ƙafafunsu, ya yafa mayafinsa, sai ya sāke kishingiɗa, ya ce musu, "Kun gane abin da na yi muku? [13]Kuna kirana Malam, da kuma Ubangiji. Daidai ne kuwa, don haka nake. [14]Tun da ya ke ni Ubangijinku, da kuma Malaminku, har na wanke muku ƙafa, ashe, ku ma ya kamata ku wanke wa juna. [15]Na yi maku ishara domin ku ma ku yi yadda na yi muku. [16]Lalle hakika, ina gaya muku, bawa ba ya fin ubangijinsa, manzo kuma ba ya fin wanda ya aiko shi. [17]In dai kun san wannan, kuna kuma aikatawa, ku masu farin ciki ne.

[34]Sabon umarni nake ba ku, shi ne ku ƙaunaci juna. Kamar yadda na ƙaunace ku, haka ku ma ku ƙaunaci juna. [35]Ta haka kowa zai gane ku almajiraina ne, in dai kuna ƙaunar juna."

## Abin da za ka Yi

Ina abu guda biyu da Yesu ya koya mana ta wurin abin da shi da kansa ya yi?

1. Ya ce, "Tun da ya ke ni Ubangijinku, da kuma Malaminku har na_______________maku_______________, ashe, ku ma ya kamata ku_______________wa_______________" (aya 14).
2. Ya ce kuma, "Kamar yadda na_______________ku, haka ku ma ku_______________juna" (aya 34).

## Asirin Yin Farin Ciki

Yesu ya ce in dai mu bi abin da ya aikata, mu yi wa waɗansu hidima mu masu farin ciki ne. Ga foton! Ga Yesu Mahalicin dukan kome, ya durkusa ya yi aikin bawa. Ya wanke kura daga ka-

faffun almajiransa! "**Ku ɗauki halin Almasihu Yesu, wanda, ko da ya ke surar Allah yake, bai mai da daidaitakan nan tasa da Allah abar da zai riƙe kankan ce ba, sai ma ya mai da kansa baya matuƙa ta ɗaukar surar bawa, da kuma kasancewa da kamannin ɗan adam. Da ya bayyana da siffar mutum, sai ya ƙasƙantar da kansa ta yin biyayya, har wadda ta kai shi ga mutuwa, mutuwar ma ta gicciye. Saboda haka ne kuma Allah ya ɗaukaka shi mafificiyar ɗaukaka** " (Filibiyawa 2:5-9a).

Bari dai mu lura, mu nemi hanyoyi inda mun iya yi wa waɗansu hidima domin bukatarsu su samu. In mun yi haka za mu yi farin ciki. Yi ma waɗansu hidima, da nuna masu ƙamna, yakan nuna lalle mu masu bin Almasihu ne, domin haka shi ya yi domin mu.

## LABARI NA 22. ALKAWARIN GUDA BIYAR MASU KYAU

**1. Yahaya 14:1-3, 6**

**[1]"Kada ku damu. Ku gaskata da Allah, ku kuma gaskata da ni. [2]A gun Ubana akwai wurin zama da yawa. Da ba haka ne ba, da na faɗa muku, domin zan tafi in shirya muku wuri. [3]In kuwa na je na shirya muku wuri, sai in dawo in kai ku wurina, domin inda nake, ku ma ku zama kuna can." [6]Yesu ya ce masa, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina."**

**2. Yahaya 14:12**

**[12]"Lalle hakika, ina gaya muku, duk wanda ke gaskatawa da ni, ayyukan da nake yi, shi ma haka zai yi. Har ma zai yi ayyukan da suka fi waɗannan, domin zan tafi wurin Uba."**

**3. Yahaya 14:13, 14**

**[13]""Duk abin da kuka roƙa da sunana kuma zan yi, domin a ɗaukaka Uban ta wurin Ɗan.**



[14]Kome kuke roƙa da sunana, zan yi shi."

4. Yahaya 14:15-17

[15]"In dai kuna ƙaunata, za ku bi umarnina. [16]Ni ma zan roƙi Uba, zai kuwa ba ku wani Mai Taimako ya kasance tare da ku har abada. [17]Shi ne Ruhu na gaskiya, wanda duniya ba ta iya samunsa, domin ba ta ganinsa, ba ta kuma san shi ba. Ku kam, kun san shi, domin yana zama tare da ku, zai kuma kasance a zuciyarku."

5. Yahaya 14:27

[27]"Na bar ku da salama. Salamata nake ba ku. Ba kamar yadda duniya ke bayarwa nake ba ku ba. Kada ku damu, kada kuma ku ji tsoro."

1. Yesu ya yi alkawari cewa zai tafi **ya shirya wuri** domin su waɗanda ke binsa (Yahaya 14:1-3, 6).
2. Yesu ya alkawarta **iko wanda ya fi nasa girma** domin shi zai tafi wurin Uban. Ruhunsa wanda ke zama cikin masu binsa zai ba da iko har za su yi ayyuka da suka fi waɗanda shi da kansa ya yi da shi ke shi mutum ɗaya ne da ke zama a duniya (Yahaya 14:12).
3. Ya alkawarta **iko cikin addu'a** ga su waɗanda ke binsa (Yahaya 14:13, 14).
4. Ya alkawarta zuwan **Mai Taimako wanda zai kasance a zuciyar almajiransa.** Zai zama cikin zuciyar kowane mai binsa, ba zai zama tare da su kurum ba, zai zauna cikinsu (Yahaya 14:15-17).
5. Ya alkawarta **salama mai girma** wanda ya fi salama wanda duniya ke bayarwa girma (Yahaya 14:27). Ba za mu ji tsoro ba, domin **"Shi wanda ke zuciyarku ya fi wanda ke duniya ƙarfi"** (1 Yahaya 4:4b).

## Abin da za ka Yi

A. Ka karanta ayoyin nan da hankali kuma. Ka mai da su kamar Yesu yana yin magana da kai, kai kaɗai. Ka ɗauke takarda, ka rubuta dukan abubuwan da Yesu ya ce shi, ko Ruhu Mai Tsarki, zai yi maka.

B. Ka zaɓi aya guda uku daga Yahaya 14 waɗanda suka faranta maka zuciya. Ka haddace su. Ka rubuta lambobin ayoyi nan:

# LABARI NA 23. LABARIN ITACEN INABI



Yahaya 15:1-11

[1]"Ni ne itacen inabi na hakika, Ubana kuwa shi ne manomi. [2]Kowane reshe a cikina da ba ya 'ya'ya, sai ya datse shi. Kowane reshe mai yin 'ya'ya kuwa yakan tsarkake shi don ya ƙara haihuwa.[3]Koyanzu ma ku tsarkakakku ne saboda maganar da na faɗa muku. [4]Ku zauna a cikina, ni kuma a cikinku. Kamar yadda reshen inabi ba ya iya 'ya'ya shi kaɗai, sai ko ya zauna a itacen inabin, haka ku ma ba za ku iya ba, sai kun zauna a cikina. [5]Ni ne itacen inabin, ku kuwa rassan. Wanda ya zauna a cikina, ni kuma a cikinsa, shi ne mai yin 'ya'ya da yawa. Domin in ba game da ni ba, ba za ku iya kome ba. [6]Duk wanda bai zauna a cikina ba, za a yar da shi can, kamar reshe, yă bushe, a kuma tattara irinsu a jefa wuta, a ƙone.[7]In kun zauna a cikina, maganata kuma ta zauna a cikinku, za ku roƙi duk abin da kuke so, za a kuwa yi muku. [8]Yadda ake ɗaukaka Ubana ke nan, in kuna 'ya'ya da yawa, ta haka kuma kuke tabbata almajiraina. [9]Kamar yadda Uba ya ƙaunace ni, haka ni ma na ƙaunace ku. To, ku zauna cikin ƙaunar da nake muku. [10]In kun bi umarnina, za ku zauna cikin ƙaunar da nake muku, kamar yadda ni na bi umarnin Ubana, na kuma zauna cikin ƙaunar da yake mini. [11]Na gaya muku haka domin farin cikina ya kasance a cikinku, farin cikinku kuma ya zama cikakke."

## Zama Cikin Kristi

In mun karɓi gafara da tsarkakewa da sabon rai cikin Yesu ta wurin bangaskiya da fari, dole ne mu ƙara ci gaba cikin bangaskiya da taimakon Ruhu Mai Tsarki dukan kwanakinmu a duniyan nan. Kada mu taɓa sa tsammani mun iya rayuwa irin ta Almasihu da ƙarfin kanmu ko iyawar kanmu. Bulus ya ce, **"Ashe, rashin azancinku har ya kai haka? Da kuka fara da Ruhu, ashe, yanzu kuma da halin mutuntaka za ku ƙarasa?"** (Galatiyawa 3:3).

Wani lokaci dole ne Yesu ya hore mu. Kila za mu sha wahala, ko wani ciwo, ko wata gwadawa, amma yana so mu ƙara ba da 'ya'ya." **"Ai, kowane irin horo, a lokacin shansa, abu ne mai baƙin ciki, ba na farin ciki ba. Amma daga baya waɗanda suka horu ta haka sukan sami kwanciyar rai wadda aikin adalci ke bayarwa"** (Ibraniyawa 12:11).

## Menene 'Ya'ya Mai Ruhaniya?

Manzon Bulus ya ce, **"Albarkar Ruhu kuwa ita ce ƙauna, da farin ciki, da salama, da haƙuri, da kirki, da nagarta, da aminci, da tawali'u, da kuma kamunkai"** (Galatiyawa 5:22, 23). Da kana roƙon Yesu ya tsarkake ka, ya cika ka da Ruhunsa kowace rana, za ka gane kana ba da irin waɗannan 'ya'ya a rayuwarka. Cikin 'ya'yan adilci akwai zuciya mai yin godiya, da mai yin waƙa, da ruhu na yin biyayya, shaida ma waɗansu, bayarwa ga aikin Allah, ba za a kashe lokaci banza ba, za a furta maganar Allah gabagaɗi, za a sami amsoshin addu'arka.

## Faɗaka Mai Karfi

In ba mu zauna cikin Almasihu ba, Yesu ya ce, "Sai a datse shi," ko "za a yar da shi, a kuma tattare irinsu a jefa wuta, a ƙone." Su waɗanda ke ba da 'ya'ya ta wurin zama cikin Almasihu su ne almajiransa (aya ta 6, da ta 8). Manzo Yahuza ya tuna mana cewa, **"Ubangiji ya ceci jama'a daga ƙasar Masar, duk da haka daga baya ya hallaka waɗanda ba su ba da gaskiya ba"** (Yahuza 5b).

Ko da shi ke ba mu iya ba da 'ya'ya da ikon kanmu, ba ya yi kyau mu duba cikin Maganar Allah, yadda mu kan duba cikin madubi don, **"Ku jarraba kanku ku gani, ko har yanzu kuna raye da bangaskiya. Ku riƙa auna kanku. Ashe, ba ku tabbata Almasihu yana cikinku ba? Sai ko in kun kasa ga gwajin!"** (2 Korantiyawa 13:5). Idan muna da Maganar Yesu a cikinmu, muna yin biyayye gareshi, za mu zama cikin ƙaunarsa (Yahaya 15:10). Idan mun sani Ruhu Mai Tsarki yana cikinmu, ba mu bukata mu ji tsoro ba, domin Ruhu Mai Tsarki yakan shaida da namu ruhu, mu 'ya'yan Allah ne. Ku tuna, ƙamna ita ce gwaji mafi girma: **"Allah shi ne ƙauna, wanda ke a dawwame cikin ƙauna kuwa, ya dawwama a cikin Allah ke nan, Allah kuma a cikinsa"** (1 Yahaya 4:16b). Allah yana ƙaunarka, "Ka zauna cikin ƙaunarsa."

# LABARI NA 24. YA ZAƁE MU, MU ZAMA ABOKANSA

Yahaya 15:12-17

[12]“Wannan fa shi ne umarnina, cewa ku ƙaunci juna kamar yadda na ƙaunace ku. [13]Ba ƙaunar da ta fi haka ga mutane, wato mutum yǎ ba da ransa saboda aminansa. [14]Ku aminaina ne in kuna yin abin da na umarce ku. [15]Nan gaba ba sauran in ce da ku bayi, don bawa bai san abin da ubangijinsa ke yi ba. Sai dai in ce da ku aminai, domin na sanar da ku duk abin da na jiyo wurin Ubana. [16]Ba ku kuka zaɓe ni ba, ni ne na zaɓe ku, na sa ku ku je ku yi ’ya’ya, ’ya’yanku kuma su tabbata, domin kome kuka roƙi Uba da sunana yǎ ba ku. [17]Na umarce ku haka domin ku ƙaunaci juna.”

# LABARI NA 25. YESU YA KOYA MANA ZA MU SHA TSANANI

Yahaya 15:18-25

[18]“In duniya ta ƙi ku, ku sani sai da ta ƙi ni kafin ta ƙi ku. [19]Da ku na duniya ne da duniya ta so abinta, amma saboda ku ba na duniya ba ne, na kuma zaɓe ku daga duniya, shi ya sa duniya take ƙinku. [20]Ku tuna da maganar da na yi muku cewa, ‘Bawa ba ya fin ubangijinsa.’ In sun tsananta mini, ku ma za su tsananta muku. Da sun kiyaye maganata, da sai su kiyaye taku ma. [21]Duk wannan za su yi muku saboda sunana, don ba su san wanda ya aiko ni ba. [22]Da ba domin na zo na yi musu magana ba, da ba su da zunubi. Amma yanzu kam, ba su da wani hanzari a kan zunubinsu. [23]Wanda ya ƙi ni ya ƙi Ubana ma. [24]Da ba domin na yi ayyuka a cikinsu da ba wanda ya taɓa yi sai ni ba, da ba su da zunubi. Amma yanzu sun gani, sun kuma ƙi mu, ni da Ubana duka. [25]An yi wannan kuwa domin a cika maganar da ke rubuce cikin Shari’arsu cewa, ‘Sun ƙi ni ba dalili.’”

Yahaya 16:1-3, 33

1“Na faɗa muku duk wannan
ne domin in kawar muku da
sanadin tuntuɓe. 2Za su fisshe
ku daga jama’a. Hakika, lokaci
ma na zuwa da kowa ya kashe
ku zai zaci bautar Allah yake
yi. 3Za su yi haka ne kuwa do-
min ba su san Uba ko ni ba.
33Na faɗa muku wannan ne do-
min a gare ni ku sami salama.
A duniya kuna shan wuya, am-
ma dai ku yi farin ciki, ai, na
yi nasara da duniya.”

## Abin da za ka Yi

1. Duniya ta ke ƙin masu bi domin su ba na______________ ba ne (15:19).
2. Yesu ya ce, “Wanda ya ƙi ni, ya ƙi______________kuma” (15:23).
3. Ko da shi ke Yesu ya yi ayyuka masu ban al’ajibi a duniya, mutanen duniya, da ba su gaskata shi ba, sun______________ sun kuma______________ Yesu duk da Ubansa ( 15:24).
4. Yadda abin yake, duniya suka ƙi Yesu ba______________ (15:25).
5. Lokaci yana zuwa sa’ad da su waɗanda suka______________ masu bi za su zaci a zuciya______________suke yi (16:2).
6. Za su yi mugayen abubuwa domin ba su______________ Uban ko Yesu ba (16:3).
7. Ko da shi ke za mu sha wuya a nan duniya, mun iya yin farin ciki domin Yesu ya yi______________da duniya (16:33).

## LABARI NA 26. YESU YA YI ADDU’A DOMINMU

Yahaya 17:1-8, 15-26

1Da Yesu ya faɗi haka, sai ya
ɗaga kai sama ya ce, “Ya Uba,
lokaci ya yi. Ka ɗaukaka Ɗan-
ka domin Ɗan ya ɗaukaka ka,
2tun da ka ba shi iko a kan
dukkan ’yan adam, yǎ ba da
rai madawwami ga duk waɗan-
da ka ba shi. 3Rai madawwami
kuwa, shi ne su san ka. Allah

Makaɗaici na gaskiya, da ku-
ma Yesu Almasihu da ka aiko.
4Na ɗaukaka ka a duniya da
yake na cika aikin da ka ba ni
in yi. 5Yanzu kuma, ya Uba, ka
ɗaukaka ni zuwa ga zatinka da
ɗaukakan nan da nake da ita
tare da kai tun kafin duniya ta
kasance. 6"Na bayyana sunanka
ga mutanen da ka ba ni daga
cikin duniya. Dā ma naka ne,
ka kuwa ba ni su, sun kuma ki-
yaye maganarka. 7Yanzu kuwa
sun san duk iyakar abin da ka
ba ni daga gare ka yake. 8Do-
min kuwa maganar da ka faɗa
mini na faɗa musu, sun kuwa
karɓa, sun kuma san kakika
na fito daga wurinka ne, sun
kuma gaskata kai ne ka aiko
ni."

15Ba na roƙonka ka ɗauke su
daga duniya, sai dai ka kare su
daga Mugun nan. 16Su ba na
duniya ba ne, kamar yadda ni
ma ba na duniya ba ne. 17Ka
tsarkake su cikin gaskiya. Ma-
ganarka ita ce gaskiya. 18Ka-
mar yadda ka aiko ni duniya,
haka ni ma na aike su duniya.
19Saboda su ne nake miƙa kai-
na, domin su ma a tsarkake su



cikin gaskiya 20"Ba kuwa wa-
ɗannan kaɗai nake roƙa wa ba,
har ma masu gaskatawa da ni
ta maganarsu, 21domin dukan-
su su zama ɗaya, kamar yadda
kai, ya Uba, kake cikina, ni
kuma nake cikinka, haka su
ma su kasance cikinmu, domin
duniya ta gaskata, cewa kai ne
ka aiko ni. 22Daukakar da ka yi
mini, ita na yi musu, domin su
zama ɗaya kamar yadda muke
ɗaya, 23ni a cikinsu, kai kuma
a cikina, domin su zama ɗaya
sosai, duniya ta gane kai ne ka
aiko ni, ta kuma gane ka ƙaun-
ce su kamar yadda ka ƙaunace
ni. 24Ya Uba, ina so waɗanda

ka ba ni, su ma su kasance tare da ni inda nake, su dubi ɗaukakata da ka yi mini, domin ka ƙaunace ni tun ba a halicci duniya ba. [25]Ya Uba mai adalci, duniya kam, ba ta san ka ba, amma ni na san ka, waɗannan kuma sun sani kai ne ka aiko ni. [26]Na sanar da su sunanka, zan kuma sanar, domin ƙaunar da ka yi mini tǎ kasance a cikinsu, ni ma in kasance cikinsu."

## Yesu Ya Yi Addu'a Dominka

Annabi Ishaya ya ce, **"Ya kuwa sha hukuncin da ya cancanci masu zunubi. Ya yi roƙo dominsu"** (Ishaya 53:12b). Yana so ya ba duka waɗanda suka gaskata shi rai madawwami (Yahaya 17:2).

Yesu ya yi addu'a domin almajiransa. Dā ya ce ma Bitrus, **"Bitrus, ya Bitrus, Shaiɗan ya nemi iznin sheƙe ku kamar alkama, ya kuwa samu. Ni kuwa na yi maka addu'a, kada bangaskiyarka ta kāsa"** (Luka 22:31, 32). Kuma kafin Yesu ya mutu, ya yi addu'a ga Uban shi kare su daga Mugun nan (Yahaya 17:15b). Ya kuma yi addu'a domin dukansu waɗanda za su gaskata da shi ta wurin maganar shaida da masu binsa za su yi. Ya yi addu'a dominka!


Yake yin addu'a dominka kullayaumi. **"Saboda haka yana da ikon ceton masu kusatowa ga Allah ta wurinsa, matuƙar ceto, tun da ya ke kullum a raye yake saboda yi musu addu'a"** (Ibraniyawa 7:25). Muna da Maceci mai girma! Ya yi addu'a mu zama ɗaya da shi, da kuma ɗaya da juna cikin ƙauna! Bari a amsa addu'arsa cikin ranka da gidanka yau.

Daga baya, sa'ad da Yesu yana yin addu'a a gonar Gatsemani, ya tambaye almajiransa, **"Ashe, ba za ku iya zama a faɗake tare da ni ko da sa'a ɗaya ba?"** (Matiyu 26:40b). Kai ma, kana yin addu'a kai kaɗai kowace rana, kana yin roƙo don su ɓatattu, da kuma jiki nasa, wato jama'ar masu bi? Ya ba mu 'yanci mu shigo gaban kursiyinsa kowace rana. **"Saboda haka sai mu kusaci kursiyin Allah na alheri da amincewa, domin a yi mana jinƙai, a kuma yi mana alherin da zai taimake mu a kan kari"** (Ibraniyawa 4:16).

# LABARI NA 27. YESU YAKE DA IKO BISA RANSA DA MUTUWARSA

Yahaya 10:17, 18

17"Domin wannan Uba ke ƙaunata, domin ina ba da raina in ɗauko shi kuma. 18Ba mai karɓe mini rai, don kaina nake ba da shi. Ina da ikon ba da shi, ina da ikon ɗauko shi kuma. Na karɓo wannan umarni ne daga wurin Ubana."



Yahaya 19:4-11

4Sai Bilatus ya sāke fitowa, ya ce wa Yahudawa, "Ga shi, zan fito muku da shi, domin ku san ban same shi da wani laifi ba." 5Sa'an nan Yesu ya fito, sāye da kambin ƙayar, da alkyabba mai ruwan jar garura. Sai Bilatus ya ce musu, "To, ga mutumin!" 6Da manyan firistoci da dogaran Haikali suka gan shi, suka ɗau kururuwa suna cewa, "A gicciye shi! A gicciye ŝhi!" Bilatus ya ce musu, "Ku tafi da shi ku da kanku, ku gicciye shi, ni kam, ban same shi da wani laifi ba." 7Yahudawa suka amsa masa suka ce, "Ai, muna da Shari'a, bisa ga Shari'an nan kuwa ya wajaba a kashe shi, saboda ya mai da kansa Ɗan Allah." 8Da Bilatus ya ji maganan nan sai ya ƙara tsorata. 9Ya sāke shiga fada, ya ce wa Yesu, "Daga ina kake?" Amma Yesu bai amsa masa ba. 10Saboda haka Bilatus ya ce masa, "Ba za ka yi mini magana ba? Ba ka sani ba ni ne da ikon sakinka, ko gicciye ka?" 11Yesu ya amsa masa ya ce, "Ba ka da wani iko a kaina in ba an ba ka daga Sama ba, saboda haka wanda ya bashe ni gare ka ya fi ka zunubi."

## Yesu Ya Iya Mutu?

Tun da shi ke Yesu Ɗan Allah ne, ya yiwu mutane su kashe shi? Ba mutumin da yake da iko akan Yesu. Sai shi da kansa yana da iko ya zaɓa mutuwa da kuma tashi daga matattu.

Yesu ya ce wa Bilatus, **"Mulkina ba na duniyan nan ba ne. Da mulkina na duniyan nan ne da barorina za su yi yaƙi kada a bashe ni ga Yahudawa. Amma hakika, mulkina ba daga nan yake ba"** (Yahaya 18:36b). Yesu ya yarda Yahudawa su kama shi. Sa'ad da suka kama shi, ya ce, **"Kuna tsammani ba ni da ikon neman taimako gun Ubana ba, nan da nan kuwa ya aiko mini fiye da rundunar mala'iku goma sha biyu? To, ta yaya ke nan za a cika Littattafai kan lalle wannan abu ya kasance?"** (Matiyu 26:53, 54). Mala'iku waɗanda suka yi masa hidima lokacin da ya yi addu'a a gonar Gatsemani, suna da iko su hallaka dukan sojoji da suka kama shi, amma Yesu ya san nufin Allah wanda ya bayana cikin Maganarsa.

Yesu da kansa ya ce, **"Lalle ne Ɗan Mutum yǎ sha wuya iri iri, shugabanni da manyan firistoci da malaman Attaura su ƙi shi, har a kashe shi, a rana ta uku kuma a tashe shi"** (Luka 9:22). Ka gani, Yesu ya mutu domin shi ne nufin Allah tun ba a yi duniya ba (Wahayin Yahaya 13:8).

Nufin Allah ne, Yesu ya ci nasara da mutuwa! **"Wato tun da ya ke 'ya'yan duk suna da tsoka da jini, shi ma sai ya ɗauki kamannin haka, domin ya hallakar da mai ikon mutuwa, wato Iblis, ta mutuwarsa, yǎ kuma 'yanta duk waɗanda tun haihuwarsu suke zaman bauta saboda tsoron mutuwa"** (Ibraniyawa 2:14, 15). Kai, kana jin tsoron mutuwa? Yesu ya mutu don ya cece ka! I, Yesu ya yi zaɓe ya ba da ransa domin ka!

## LABARI NA 28. AN GICCIYE YESU, AN BINNE SHI

**Yahaya 19:17, 18, 30-37**

**17Sai suka tafi da Yesu. Ya**
**kuwa fita, shi kansa ke ɗauke**
**da gicciyensa, har zuwa wurin**
**da ake kira Wurin Koƙwan Kai,**
**da Yahudanci kuwa, Golgota.**
**18Nan suka gicciye shi, da**
**kuma waɗansu mutum biyu ta-**
**re da shi, ɗaya ta kowane gefe,**
**Yesu kuwa a tsakiya. 30Da Ye-**
**su ya tsotsi ruwan tsamin nan**
**ya ce, "An gama!" Sa'an nan**
**ya sunkuyar da kansa ya ba da**
**ransa. 31Da ya ke ran nan ra-**
**nar shiri ce, don kada a bar ji-**
**kuna a gicciye ran Asabar (do-**
**min wannan Asabar ɗin babbar**
**rana ce), sai Yahudawa suka**
**roƙi Bilatus a karya ƙafafunsu,**
**a kuma ɗauke jikunan. 32Sai so-**
**ja suka zo suka karya ƙafafun**

**na farkon nan, da kuma na ɗa-
yan da aka gicciye tare da shi.
33Amma da suka zo wurin Yesu,
suka kuma ga ya riga ya mutu,
ba su karya ƙafafunsa ba.34Sai
dai ɗaya daga cikin sojan nan
ya soke shi da mashi a kwiɓi,
nan da nan ga jini da ruwa su-
ka gudano. 35Wanda ya gani ɗin
kuwa ya ba da shaida kan ha-
ka, shaida tasa kuwa gaskiya
ce, ya kuma san gaskiya yake
faɗa, domin ku ma ku ba da
gaskiya. 36Wannan kuwa don a
cika Nassi ne cewa, "Kashinsa
ɗaya ba za a karya ba." 37Wani
Nassi kuma ya ce, "Za su dubi
wanda suka soka."**

**Yahaya 19:40-42**

**40Sai suka ɗauki jikin Yesu**



**suka sa shi a likkafanin lilin
game da kayan ƙanshin nan,
bisa ga al'adar Yahudawa ta
jana'iza. 41A wurin da aka gic-
ciye shi kuwa akwai wani lam-
bu, a cikin lambun kuma da
wani sabon kabari wanda ba a
taɓa sa kowa ba. 42Da ya ke
ranar shiri ce ta Yahudawa,
kabarin kuma na kusa, sai su-
ka sa Yesu a nan.**

## Mutuwar Yesu Ba Wani Haɗari Ba

Mabuɗin fahimta Maganar Allah, shi ne a gane cikin dukan Maganar Yesu shi me matsaka. **"Sai ya fara ta kan littattafan Musa da na dukan annabawa, ya yi ta bayyana musu abubuwan da suka shafe shi a dukan Littattafai"** (Luka 24:27). Yesu ya sani, **"Ya kuma ce musu, Wannan ita ce maganata da na gaya muku tun muna tare, cewa lalle ne a cika duk abin da ke a rubuce game da ni a Attaura ta Musa, da littattafan annabawa, da kuma Zabura"** (Luka 24:44). **"Sa'an nan ya wayar da hankalinsu su fahimci Littattafai, ya kuma ce musu, Haka yake a rubuce, cewa wajibi ne Almasihu ya sha wuya, a rana ta uku kuma ya tashi daga matattu, a kuma yi wa dukan al'ummai wa'azi su tuba, a gafarta musu zunubansu saboda sunansa. Za a kuwa fara daga Urushalima"** (Luka 24:45-47).

Nufin Allah abu mai kyau ƙwarai! Idan kana da Littafi Mai Tsarki ka bincike waɗannan ayoyi don ka gani yadda Allah ya nuna ma duniya nufinsa cikin Tsohon Alkawari da yadda Yesu ya cika nufinsa. (Daga cikin annabci wajen 300 da annabawa suka faɗi, su kaɗan ne batun zuwan Yesu na fari cikin duniya.)


Shaiɗan ya ruɗi mutumin Allah na fari, amma Allah ya san yadda zai cece shi. Wannan shiri da Allah ya yi, ya ci nasara. Duk waɗanda suna so Allah ya cece su daga hannun Shaiɗan zai cece su.

| **Shirin Allah** | **Annabci** | **Cikawa** |
|---|---|---|
| Alkawarin "zuriya mace" | **Farawa 3:15** | **Galatiyawa 4:4** |
| Alkawarin "zuriyar Ibrahim" | **Farawa 18:18** | **Ayyuka Man 3:25** |
| Haifuwa a Baitalami | **Mika 5:2** | **Matiyu 2:1** |
| Haifuwar Budurwa | **Ishaya 7:14** | **Matiyu 1:18** |
| Aikinsa a Galili | **Ishaya 9:1, 2** | **Matiyu 4:12-16** |
| Zai zama annabi | **Maimaitawar Shari'a 18:15** | **Yahaya 6:14** |
| Zai zama firist | **Zabura 110:4** | **Ibraniyawa 6:20** |
| Zai zama sarki | **Ishaya 9:7** | **Yahaya 18:36, 37** |
| Yahudawa za su ƙi shi | **Ishaya 53:3** | **Yahaya 1:11; 5:43** |
| Shigowar Urushalima | **Zakariya 9:9** | **Yahaya 12:13-15** |
| Aboki zai ba da shi | **Zabura 41:9** | **Markus 14:10** |
| Za a sayar da shi don tsabar azurfa talatin | **Zakariya 11:12** | **Matiyu 26:15** |
| Masu shaidar zur suka yi ƙara | **Zabura 27:12** | **Matiyu 26:60, 61** |
| Ya yi shiru | **Ishaya 53:7** | **Matiyu 26:62, 63** |
| An duke shi, an tofa masa yau | **Ishaya 50:6** | **Markus 14:65** |
| An gicciye shi da masu zunubi | **Ishaya 53:12** | **Matiyu 27:38** |
| An soke hannuwa da kafaffu | **Zabura 22:16** | **Yahaya 20:27** |
| An yi ba'a da raini | **Zabura 22:6-8** | **Matiyu 27:39, 40** |
| An ba shi ruwan tsami | **Zabura 69:21** | **Yahaya 19:29** |
| Ya yi addu'a don magabta | **Ishaya 53:12** | **Luka 23:34** |
| Suka soke shi | **Zakariya 12:10** | **Yahaya 19:34** |
| Ba za a karye ƙashi | **Zabura 34:20** | **Yahaya 19:33** |
| An binne shi tare da masu arziki | **Ishaya 53:9** | **Matiyu 27:57-60** |
| Tashinsa daga matattu | **Zabura 16:10** | **Matiyu 28:9** |
| Tashinsa zuwa sama | **Zabura 68:18** | **Luka 24:50, 51** |

(Don cikakken labarin mutuwar Yesu, karanta Matiyu 26 da 27; Markus 14 da 15; Luka 22 da 23; Yahaya 18 da 19; Ishaya 53; da Zabura 22.)

# LABARI NA 29. YESU YA TASHI DAGA MATATTU

Yahaya 20:1-9



1To, a ranar farko ta mako,
Maryamu Magadaliya ta je ka-
barin da asuba, tun da sauran
duhu, ta ga an kawar da dut-
sen daga kabarin. 2Sai ta yiwo
gudu wurin Bitrus da kuma al-
majirin nan da Yesu ke ƙauna,
ta ce musu, "An ɗauke Uban-
giji daga kabarin, ba mu kuwa
san inda aka sa shi ba." 3Sai
Bitrus da almajirin nan suka
fita suka doshi kabarin. 4Duka
biyu suka ruga a guje, amma
almajirin nan ya tsere wa Bi-
trus, ya riga isa kabarin. 5Yana
duƙawa yana leƙa ciki, sai ya ga
likkafanin lilin a ajiye, amma
fa bai shiga ba. 6Sa'an nan
Bitrus ya zo a bayansa, ya ku-
wa shiga kabarin, ya ga likka-
fanin a ajiye, 7mayanin kuma
da ke kansa ba a ajiye tare da
likkafanin yake ba, amma a
naɗe shi kaɗai a waje ɗaya.
8Sai almajirin nan da ya riga
isa kabarin shi ma ya shiga, ya
gani, ya kuma ba da gaskiya.
9Don kafin lokacin nan ba su
fahimci Nassin nan ba, cewa
lalle ne yǎ tashi daga matattu.

## Ga Dalilin Da Tashin Matattu Muhimmin Abu Ne

Tun dā Ayuba ya yi tambaya, **"Idan mutum ya mutu, zai sāke rayuwa kuma?"** (Ayuba 14:14). Wannan kuma amsarsa, **"Amma na sani akwai wani a Samaniya wanda a ƙarshe zai zo ya tsaya mini. Ko da ya ke ciwo ya riga ya cinye fatata, a wannan jiki zan ga Allah"** (Ayuba 19:25, 26). I, domin shi ya rayu, mu kuma za mu rayu (Yahaya 14:19).

**"Ko da ya ke an gicciye shi ne da rashin ƙarfi, duk da haka a raye yake ta ikon Allah. Mu ma marasa ƙarfi ne kamarsa, amma game da al'amuranku da za mu zartar, a raye muke tare da shi, ta ikon Allah"** (2 Korantiyawa 13:4).

Dukan labari mai daɗi, Bulus ya taƙaita cikin aya biyu da cewa: **"Jawabi mafi muhimmanci da na sanar da ku, shi ne wanda na karɓo, cewa Almasihu ya mutu domin zunubanmu, kamar yadda Littattafai suka faɗa, cewa an binne shi, an ta da shi a rana ta uku, kamar yadda Littattafai suka faɗa."** (1 Korantiyawa 15:3, 4). Da ba domin tashin Yesu Almasihu daga matattu, ba mu da labarin da za mu yi wa'azinsa ba. Da ba mu da bege. Da muna zauna cikin zunubanmu, da hukunci rabonmu. Amma, godiya ga Allah, Yesu yana da rai, shi ya iya zauna cikinmu! **"In kuwa Ruhun wannan da ya ta da Yesu daga matattu na zaune a zuciyarku, to, shi da ya ta da Almasihu Yesu daga matattu zai kuma raya jikin nan naku mai mutuwa, ta Ruhunsa da ke zaune a zuciyarku"** (Romawa 8:11).

## Yanzu Sai Mu Rayu Dominsa

**"Kaunar Almasihu gare mu ita ke mallakarmu, saboda haka mun tabbata, da ya ke wani ya mutu saboda dukan mutane, ashe kuwa, mutuwa tasu ce dukansu. Ya kuwa mutu ne saboda dukan mutane, domin waɗanda ke raye, kada su yi zaman ganin dama nan gaba, sai dai su yi zaman wannan da ya mutu saboda su, aka kuma tashe shi saboda su"** (2 Korantiyawa 5:14, 15). Dā mu matattu ne cikin zunubanmu, amma Yesu ya mutu domin mu. Yanzu Yesu ya rayad da mu. Mu sabon halitta ne. Kada mu rayu don kanmu, amma mu rayu dominsa. Mu ba na kanmu mu ke ba. **"Sayenku aka yi da tamani. To, sai ku ɗaukaka Allah da jikinku"** (1 Korantiyawa 6:20).

## LABARI NA 30. YESU YA BAYANA GA MARYAMU

Yahaya 20:11-17

11 Maryamu kuwa na tsaye a bakin kabarin daga waje, tana kuka. Tana cikin kuka sai ta duƙa ta leƙa kabarin, 12 sai ta ga mala'iku biyu saye da fararen tufafi a zaune inda dā gawar Yesu yake, ɗaya wajen kai, ɗaya kuwa wajen ƙafafu. 13 Suka ce mata, "Uwargida, don me kike kuka?" Ta ce musu, "Ai, an ɗauke Ubangijina, ban kuwa san inda aka sa shi ba." 14 Da ta faɗi haka sai ta juya ta ga Yesu tsaye, amma ba ta gane Yesu ne ba. 15 Yesu ya ce mata, "Uwargida, don me kike kuka? Wa kike nema?" Saboda kuma



ta zaci shi ne mai aikin lambun, ta ce masa, "Maigida, in kai ne ka ɗauke shi, gaya mini inda ka sa shi mana, ni kuwa in ɗauke shi." 16Yesu ya ce mata, "Maryamu!" Sai ta juya ta ce masa da Yahudanci, "Rabboni!" wato Malam. 17Yesu ya ce mata, "Kada ki riƙe ni, domin har yanzu ban hau wurin Uba ba tukuna. Sai dai ki tafi wurin 'yan'uwana ki ce musu ina hawa wurin Ubana kuma Ubanku, Allahna kuma Allahnku."

## Yadda Yesu Ya Ba Da Girma Ga Mataye

Cikin lokacin ban tausayi, ko cikin lokacin farin ciki Yesu ya girmama mataye. Lokacin da aka gicciye shi, Yesu yi yi magana da uwarsa, ya miƙa ta a hannuwan almajiran da ya fi ƙaunarsa (Yahaya) don ya lura da ita (Yahaya 19:26, 27). Yanzu da ya yi nasara da mutuwa, ya tashi ya bayana ga mace da fari–wata Maryamu.

Mataye, masu bin Allah, masu ado na tawali'u da natsuwa, **"wannan kuwa abu ne mai martaba ƙwarai a gun Allah"** (1 Bitrus 3:4). Lokacin da Allah ya halitta mutum cikin surar kansa ya hallici mutum, namiji da ta mace cikin siffarsa (Farawa 1:27). Cikin abubuwa masu ruhaniya, Allah ya ba dukansu biyu, namiji da ta mace dama daidai da juna su zo su karɓi gado daidai da juna. **"Waɗanda kuma ta wurinsu ya yi mana baiwa da manyan alkawaransa masu ɗaukaka ƙwarai, domin ta wurin waɗannan ku zama masu tarayya da Allah wajen dabi'arsa"** (2 Bitrus 1:4a). **"Ba sauran cewa...ko mace ko namiji. Ai, dukkanku ɗaya kuke, na Almasihu Yesu"** (Galatiyawa 3:28b).

Allah ya ba da girma ga mataye har ya yi umurni cewa mazaje su ƙaunace matansu yadda Almasihu ya ƙaunaci ikilisiya, har ya ba da ransa dominta (Afisawa 5:25). **"Ta haka ya wajaba maza su ƙaunaci matansu, jikinsu ke nan suke yi wa. Ai,**

**wanda ya ƙaunaci mata tasa, ya ƙaunace kansa ke nan"** (Afiswa 5:28). Allah yake so jituwa mai kyau tsakanin namiji da matarsa. Ya ƙi kisan aure. **"Ni Ubangiji Mai Runduna, Allah na Isra'ila, na ce ina ƙin kisan aure"** (Malakai 2:16a). **"To, albarkacinsu ku cikasa farin cikina da zamanku lafiya da juna, kuna ƙaunar juna, nufinku ɗaya, ra'ayinku ɗaya. Kada ku yi kome da sonkai ko girmankai, sai dai da tawali'u, kowa na mai da ɗan'uwansa ya fi shi"** (Filibiyawa 2:2, 3).

## LABARI NA 31. YESU YA BAYANA GA ALMAJIRANSA

**Yahaya 20:19-22**




**[19]A ran nan da magariba, ranar farko ta mako, ƙofofin ɗakin da almajiran ke ciki na kulle don tsoron Yahudawa, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsaka, ya ce musu, "Salamu alaikun!" [20]Da ya faɗi haka, ya nuna musu hannuwansa da kwiɓinsa. Sai almajiran suka yi farin ciki da ganin Ubangiji. [21]Sai Yesu ya sāke ce musu, "Salamu alaikun! Kamar yadda Uba, ya aiko ni, haka ni ma na aike ku." [22]Da ya faɗi haka ya busa musu numfashinsa, ya ce musu, "Ku karɓi Ruhu Mai Tsarki."**

## Abin da za ka Yi

Me Yesu ya ce? Cika filayen nan.

1. Ya ce musu "____________________" (aya ta 19).
2. "Kamar yadda Ubangiji ya aiko ni, haka____________________ ____________________" (aya ta 21).
3. "____________________Ruhu Mai Tsarki" (aya ta 22).

# LABARI NA 32. MAI YIN SHAKKA YA GASKATA



Yahaya 20:24-29

[24]Toma kuwa, ɗaya daga cikin sha biyun nan, wanda ake kira Ɗan Tagwai, ba ya nan tare da su sa'ad da Yesu ya zo. [25]Sai sauran almajiran suka ce masa, "Mun ga Ubangiji." Amma ya ce musu, "In ban ga gurbin ƙusoshi a hannuwansa ba, in sa yatsana a gurbin ƙusoshin, in kuma sa hannuna a kwiɓinsa ba, ba zan ba da gaskiya ba."

[26]Bayan kwana takwas har wa yau almajiransa na cikin gidan, Toma ma na nan tare da su, ƙofofi na kulle, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsaka, ya ce, "Salamu alaikun." [27]Sa'an nan ya ce wa Toma, "Sa yatsanka nan, ka ji hannuwana. Miƙo hannunka kuma ka sa a kwiɓina. Kada ka zama marar ba da gaskiya, sai dai mai ba da gaskiya." [28]Toma ya amsa masa ya ce, "Ya Ubangijina, Allahna kuma!" [29]Sai Yesu ya ce masa, "Wato saboda ka gan ni ka ba da gaskiya? Albarka tā tabbata ga waɗanda ba su gani ba, amma kuwa suka ba da gaskiya."


## Albarka Mai Kyau

Yesu ya ce yana da albarka mai kyau ga wanda ya gaskata shi ko ba a gan shi da idonsa ba. Yau mun san Yesu ta wurin Ruhunsa wanda ke zamne cikinmu. Mun san shi kuma ta wurin Maganarsa (Littafi Mai Tsarki).

Wata rana za mu gan shi. **"Amma mun sani sa'ad da ya bayyana za mu zama kamarsa, domin za mu gan shi kamar yadda yake"** (1 Yahaya 3:2b). **"Albarka tā tabbata ga masu tsarkakakkiyar zuciya, domin za su ga Allah"** (Matiyu 5:8). **"Ga shi, zai zo a cikin gajimare, kowa zai gan shi, har da waɗanda suka soke shi, duk kabilan duniya kuma za su yi kuka a kansa. Wannan haka yake. Amin"** (Wahayin Yahaya 1:7). Lokacin da ka ga Yesu, za ka yi murna ko baƙin ciki? Idan Yesu shi ne Ubangijinka da Allahnka, yadda shi na Toma ne, za ka yi murna ƙwarai!

# LABARI NA 33. YESU YANA DA IKON BIYA BUKATA

Yahaya 21:2-6, 9-12, 15-17
[2]"Bitrus, da Toma wanda ake
kira Ɗan Tagwai, da Nata'ala
na Kana ta ƙasar Galili, da
'ya'yan nan na Zabadi, da ku-
ma waɗansu almajiransa biyu,
duk suna nan tare. [3]Sai Bitrus
ya ce musu, "Za ni sū." Suka
ce masa, "Mu ma mā tafi tare
da kai." Sai suka fita suka shi-
ga jirgi. Amma a daren nan ba
su kama kome ba. [4]Gari na
wayewa sai ga Yesu tsaye a ba-
kin gaci, amma almajiran ba
su gane Yesu ne ba. [5]Sai Yesu
ya ce musu, "Samari, kuna da
kifi?" Suka amsa masa suka
ce, "A'a." [6]Ya ce musu, "Ku
jefa taru dama da jirgin za ku
samu." Suka jefa, har suka ka-
sa jawo shi don yawan kifin.
[9]Da fitowarsu gaci sai suka
ga garwashi a wurin, da kifi a
kai, da kuma gurasa. [10]Yesu ya
ce musu, "Ku kawo waɗansu



kifi a na waɗanda kuka kama
yanzu." [11]Sai Bitrus ya hau jir-
gin, ya jawo tarun gaci, cike
da manyan kifaye, ɗari da
hamsin da uku. Amma duk da
yawansu haka, tarun bai kece
ba. [12]Sai Yesu ya ce musu, "Ku
zo ku karya kumallo." Daga
cikin almajiran kuwa ba wan-
da ya yi ƙarfin halin tamba-
yarsa ko shi wanene, domin
sun sani Ubangiji ne.
[15]Da suka karya kumallo Ye-
su ya ce wa Bitrus, "Bitrus ɗan
Yahaya, ka fi waɗannan ƙau-
nata?" Ya ce masa, "I, ya U-
bangiji, ka dai sani ina sonka."
Yesu ya ce masa, "Ka yi kiwon
'ya'yan tumakina." [16]Ya sāke
faɗa masa, faɗa ta biyu, "Bi-
trus ɗan Yahaya, kana ƙauna-
ta?" Ya ce masa, "I, ya Uban-
giji, ka dai sani ina sonka."
Yesu ya ce masa, "Ka kiyaye
tumakina." [17]Yesu ya faɗa ma-
sa, faɗa ta uku, "Bitrus ɗan
Yahaya, kana sona?" Sai Bi-
trus ya yi baƙin ciki don a fa-
ɗan nan ta uku ya ce masa,
"Kana sona?" Shi kuwa ya ce
masa, "Ya Ubangiji, ai, ka san
kome duka, ka kuwa sani ina
sonka." Yesu ya ce masa. "Ka
yi kiwon tumakina."

## Zo, Ka Ci

Wannan foto mai kyau ne inda Yesu yana gayyaci almajiransa su zo su ci abinci. Yesu ya kira su ga wuri inda za a biya masu bukatarsu. Kai ma kana jin yunwa da kishin ruwa don adalci? Yesu ya ce, **"Albarka tā tabbata ga masu kwaɗaita ga adalci, domin za a biya musu muradi"** (Matiyu 5:6).

Ku zo wurinsa kowace safiya don ka ci Maganarsa har ka ƙoshi. Ubangijinka da Allahnka wanda ya cece ka daga bautar Shaiɗan yana ce maka, **"Ku buɗe bakinku, zan ciyar da ku"** (Zabura 81:10b).

Idan kai na Almasihu ne akwai wani lokaci da zai gayyace ka, "Zo, ka ci." Kafin Yesu zai dawo duniya SARKIN SARAKUNA da UBANGIJIN IYAYENGIJI, zai gayyace ku, ku zo bikin Ɗan Ragon.

**"Mu yi ta murna da farin ciki matuƙa, mu kuma ɗaukaka shi, domin bikin Ɗan Ragon nan ya zo, amarya tasa kuma ta kintsa. An yardar mata ta sa tufafin lallausan lilin mai ɗaukar ido, mai tsabta. Lallausan lilin ɗin nan shi ne aikin adalci na tsarkākā."** (Wahayin Yahaya 19:7, 8). Kana da shiri don wannan biki? Ka tuna, ba mu iya yafe adalcin kanmu domin a ganin Allah adalcin kanmu ya zama kamar **"ƙazamai ne duka"** (Ishaya 64:6b). Adalcin Yesu da kansa kaɗai ya isa ya mai da mu masu isa mu shiga wurin bikin Ɗan Ragon nan. **"Shi da bai san zunubi ba, Allah ya mai da shi zunubi saboda mu, domin mu mu sami adalcin Allah ta wurinsa"** (2 Korantiyawa 5:21). Ya ɗauke namu zunubi, ya ba mu nasa adalci!

## Yi Kiwon Tumakina

Bayan Yesu ya ciyad da ku, yana so ku ciyad da waɗansu. An ciyad da ku ta wurin koyarwan nan na Bisharar Yahaya? Sai ka gaya ma waɗansu abin da Allah ya koya maku. **"Ku yi kiwon garken Allah da ke tare da ku . . . ku zama abin koyi ga garken nan"** (1 Bitrus 5:2a, 3b). Mun iya zama abin albarka ga waɗansu idan mun yi kiwon su, mu zama abin koyi garesu. **"Kuna koya musu su kiyaye duk iyakar abin da na umarce ku. Ga shi, ni kuma kullum ina tare da ku har matuƙar zamani"** (Matiyu 28:20).

# Amsoshin Tambayoyi

Amsoshin tambayoyi da ke cikin wannan koyarwa suna nan kasa, domin ka gwada ko amsoshinka ke daidai. Ka duba waɗannan bayan da ka riga ka ba da amsoshi duka da kanka.

**Shafi 4, 5**

1. Allah
2. tare da Allah
3. Rai
4. Duhu
5. Yahaya
6. Jama'a tasa
7. 'Ya'yan Allah
8. da jini, kwaɗayin jiki nufin mutum, Allah
9. Mutum
10. a cikin mu
11. falala tasa, alheri, alheri
12. Ɗa

**Shafi 8, 9**

1. Murya, jeji
2. Miƙe, Ubangiji
3. bayana, shugabana
4. Ɗan Rago, Allah, zunubin, duniya
5. Isra'ila
6. kurciya, Ruhu Mai Tsarki

**Shafi 14**

1. Duk abin da ya ce ku yi, sai ku yi.
2. fal

**Shafi 21, 22**

1. Bafarisiye, ko wani shugaban Yahudawa, da dad dare
2. malami
3. sake haifuwa
4. ruwa, Ruhu
5. mutum
6. ruhu
7. Musa, macijin
8. ƙaunar, hallaka rai madawwami
9. yanke hukunci, sami ceto
10. Za a yi masa hukunci, ba da gaskiya
11. duhu, haske mugaye, hukunci
12. Mai aikata gaskiya

**Shafi 28, 29**

1. Ya gaji.
2. Sa mini ruwa in sha.
3. Yahudawa ba su yi cuɗanya da Samariyawa.
4. ruwan rai
5. Duk mai shan ruwan nan zai sake jin ƙishirwa, amma duk wanda ya sha ruwan da zan ba shi, ba zai zai ƙara jin ƙishirwa ba har abada.
6. Ta yi miji biyar, wanda ta ke da shi ba mijinta ba ne.
7. sujada
8. A ruhu da gaskiya.
9. Ta koma gari, ta gaya wa mutane batun Yesu.
10. Ya zo don ya aikata nufin Ubansa, ya kuma cika aikinsa.
11. Shi ne Mai Ceton duniya.

**Shafi 34**

1. 38
2. warkar
3. dauƙe, tafiya
4. Ka daina yin zunubi
5. a. keta, Asabar
   b Ubansa ne

**Shafi 42**

1. zauna, almajirai
2. gaskiya
3. bawan zunubi
4. Ɗan
5. ƙaunace
6. Allah
7. nufin, san koyarwa

**Shafi 44, 45**

1. Yesu
2. Maƙwata
3. Farisawa
4. Iyayensa
5. Makaho
6. Yesu
7. Makaho

**Shafi 61**

1. Wanke, kafa, ku wanke, juna
2. Ƙaunace, ƙaunaci

**Shafi 67**

1. duniya
2. Ubana
3. gani, ƙi
4. dalili
5. kashe, bautar Allah
6. san
7. nasara

**Shafi 77**

1. Salama alaikun
2. na aike ku
3. Ku karɓi

Bible text is from the Bible in Hausa, *Littafi Mai Tsarki*, ©1979 by the United Bible Societies, Africa Regional Centre, Nairobi, Kenya. Used by permission.

Published in numerous languages by World Missionary Press, Inc., as God supplies funds in answer to prayer. **For questions or more information by country, visit: www.wmp-contacts.org**

Wannan littafi ba domin a rarraba ga mutane kowa da kowa. Yana domin kai, ko wasu mutane kima su bincike su tare.

Kyauta—Kada a sayar

World Missionary Press
PO Box 120
New Paris, IN 46553-0120 USA
www.wmpress.org

Read booklets online or by App
www.wmp-readonline.org

4-25

1311/2 Hausa BSJ